
# LITTAFIN HORARWA GA 'YAN-AGAJIN ADALCI GAME DA



# INGANTA SAMAR DA ADALCI GA MATAN AREWACIN NAJERIYA

## NA
## GLOBAL RIGHTS NIGERIA

# LITTAFIN HORARWA GA 'YAN-AGAJIN ADALCI GAME DA
## *Inganta Samar da Adalci ga Matan Arewacin Najeriya*

**Na**

**GLOBAL RIGHTS NIGERIA**

**WALLAFAWA DA BUGAWA**

**GLOBAL RIGHTS NIGERIA**

**HAKKIN MALLAKAR M**
**GLOBAL RIGHTS 2012**

Dukkan Hakki na me mallaka ne. An amince za'a iya sake gurza abinda ke cikin wannan littafi ko kuma a dan gutsuro wani bayani daga cikin littafin ma-damar an bada isasshiyar manuniya ga asalinshi wato hakkin malaka.

Ra'ayoyin da aka bayyana cikin wannan littafin na Global Rights ne, ba lalle bane su zama ra'ayoyin masu bamu gudun-muwa. daomin karin bayani a tuntubi sashen Sadarwa na Global Right akan lambar waya: +1(202) 822-4000 ko ofishin mu na Najeriya akan: +23497830116.

An fara bugawa a Najeriya da turanci, 2010

An fassara zuwa Hausa a Najeriya, 2012

Cikakkar Lambar Littafi ta Duniya ISBN……………………………………..

**Game da Kungiyar Global Rights**

An kirkiro kungiyar Global Rights a shekarar 1978, ta kasance ita kungiyace mai bayar da horarwa game da ‘yancin dan-adam. Kuma tana aiki kafada da kafada da masu gwagwarmayar kare hakki a yankunan Afirka, da Asiya da kuma Latin Amurka don ingantawa da kare hakkin al-ummu marasa rijaye. kungiyar tana yin hakane to hanyar bada taimako irin na kwararru gami da horarwa. Muna karfafa gwiwar abokan hulgarmu wajen tattara bayanai tare da fallasa wuraren da aka keta hakkin dan-adam. Muna gudanar da abinda ya danganci zurfafawa da fadadawa don gamewa da duk al-ummun da sha’anin mu ya shafa, tare da wayar da kai da ilmantarwa game da tsarin doka da kuma samar da sauyi mai ma’ana, hadi da gudanar da aiyukan da suka shafi adalci da agajin adalci.

A bisa tarihin mu na fiye da shekaru talatin, munyi aikace-aikace a kasashe daban-daban don taimaka ma jagororin al’umma da kungiyoyi wajen warware matsalolin keta hakkin dan-adam da kuma habaka yunkurinsu ta hanyar hada su da takwarorinsu na nahiya da na duniya baki daya a inda manyan hukomomin irinsu Majilisar dinkin duniya da kuma kungiyar hadin guiwa ta jahohin Amirka suke kirkirawa gami da zartar da dokokin kare hakkin dan-adam,

Kokuwar al’amarinmu shine tsantsar sadaukar da kai don ci gaban samarda adalci ga matalauta da bangarori marasa rinjaye, tare da jan ragamar samar da adalci ga mata, tabbatar da daideto tsakanin maza da mata, da ci gaban kawar da kabilanci da bangaranci. Bugu da kari, muna da wani yunkuri na musamman a kan ‘yancin mata masu sha’awar junansu, maza masu sha’awar junansu, mata-maza da ‘yan daudu. Sai kuma ‘yanci akan Ma’adanai da ‘yancin dan-adam. Wannan ya bamu damar mu kwarari wannan sabon fage a yayin da muke kokarin cimma jama’ar da al’amarin mu ya shafa.

**ABUBUWAN DA KE CIKI**


**Mukaddima** 6

**Tsokaci Game da Wannan Littafi** 7
**Haruffa Masu Wakiltar Sunaye** 8

**BABI NA 1: SANIN AIKIN 'YAN AGAJIN ADALCI** 11

**BABI NA 2: DABARUN TAIMAKON BADA SHAWARA DANA SASANCI** 16

**BABI NA 3: TSARIN DOKAR NAJERIYA** 21

**BABI NA 4: DOKAR IYALI** 27

**BABI NA 5: GADO** 41

**BABI NA 6: HAKKIN MATA DA HAKKIN DAN-ADAM** 45

**BABI NA 7: DOKAR LAIFUKA** 57

**BABINA 8: DOKAR LAIFUKA KAMU DA BELI** 60

**BABI NA 9: SAURAN MATSALOLI DA SUKA SHAFI MATA** 63

**BABI NA 10: JERIN LITATTAFAN DA KE DA NASABA DA WANNAN LITTAFI** 68

**BABI NA 11: KAMU DA TSAREWA** 76

**MUKADDIMA**

Aikin agajin-adalci a al’umance yana da alaka da bukatar da ke akwai wajen bunkasawa da kare hakkin can adam tare da sammar da adalci managarci ga al’umomi na matakin farko, musamman ma ga marasa rinjaye, marasa galihu da matalauta.

Aikin agajin adalci yana kuma taimaka ma tabbatar da aikin gaskiya da gaskiya a cikin tsarin shari’a. Ta hanyar aiyukan Agajin-adalci a al’umance, akan samu wadatuwar taimako da shawarwari a harkar doka musamman ga matan karkara.

Bayan sun kamala samun horo, anasa ran ‘Yan Agajin-adalci su rika bayar da taimako da shawarwari game tsarin shari’a. Sannan kuma ma’aikatan shari’a da lauyoyi zasu rika kiwon al’amarin su, tare da masana hakkin can adam, wajen gudanar da aiyukan su. Akwai bukatar ‘Yan-agajin adalci su kai wani mataki na ilimi ko kwarewar aiki ta yadda zasu iya gudanar da aiyukansu cikin nasara. Don a samu fa’idar aikin ana bukatar ‘Yan-agajin su zamo mazauna yankin da suke aiki. Hakan zai inganta samun karbuwar su ga jama’ar da suke aiki cikinsu, zai kuma taimaka wurin samun kyakkyawar fahimtar matsalolin mutanen dai-dai da muhallinsu.

Duk da yake dai ana kara samun kyakkyawar fahimta game da muhimmancin aikin agajin adalci a Najeriya, al’amarin dai yana tafiyar hawainiya. ‘Yan-agajin adalci sun rika samun matsaloli a baya saboda ba ko ina ne aka san su kuma aka amince dasu ba a facin kasar nan. Don haka, a yanzu haka akwai yunkuri da akeyi don samun gindin zama a gwamnatance ga ‘yan agajin-adalci, tun da yake ma kimanin jihohin Nijeriya 27 daga cikin 36 nada ‘yan agajin adalci a matakin farko na al’umma. Madamar ana samun karbuwa, to aikin ‘yan agajin-adalci zai samu kuarin darattawa da shiga rai ga al’ummomi a duk facin kasar nan.

## TSOKACI GAME DA WANNAN LITTAFI

An shirya wannan littafi ne musamman don a dinke barakar da aka gano daga nazarin da kungiyar Global Rights ta gudanar a shekarar 2009, mai taken “Awon mizani don gano mafi rinjaye daga cikin matsalolin shari’a ga matan arewacin Najeria”. Kuma an tsara littafin ne don amfanin kungiyoyin al’umma, ‘yan gwagwarmayar kare hakkin dan-adam da jagororin mabiya ra’ayoyi daban-daban a matakin farko na al’umma. Littafin na dauke da isasshen bayani mai ilmantarwa game da samar da adalci ga mata, ‘yancin dan-adam da kuma tsarin doka. Manufar littafin shine tallafawa ‘yancin mata tare da samara da adalci ga matan arewacin Najeriya. Shi wannan littafi daya ne daga cikin kokarin kungiyar Global ‘right don tallafa ma ‘yancin dan-adam da adalci ga alummomin matakin farko na Najeriya.

An shirya bayanan dake cikin wannan littafi ne don amfanin masu bada horarwa ga ‘yan-agajin adalci da kuma masu koyon aikin agajin adalci. Littafin horarwa, wanda ke tafiya kafada-da-kafada da wannan littafi, wanda mai bada horarwa ke amfani da shi, yana kunshe da wasu aiyuka da ake yi a ajin horarwa, irinsu aikin hadin gwiwa, da jarraba yadda mutum zai gudanar da aiki, da wasan kwaikwayo, da binciken mafita akan wasu matsaloli abin kwantanci, da wasa kwakwalwa, da tattaunawa.

Littafin yana karfafa gwiwar mahalarta horarwa akan abubuwa makamantan:

- Yin nazari da tunani game da al’amuran da suka shafi hakkin dan-adam.
- Fahimtar ko menene hakkin mata da kuma hanyoyin da za’a iya kare shi.
- Fahimtar muhimmacin kowane jinsi da gudunmuwar da zasu iya badawa.
- Kusantar da doka ga Wanda ta shafa.
- Fahimtar al’amarin isar da adalci ga mata.
- Fahimtar hanyoyin dake akwai don warware matsalolin keta haddi.
- Gano hanyoyin da za’a iya fa’idantuwa da ilmin da aka samu a cikin harkokin yau da kullum.

An shirya wannan littafi ne don amfani wurin aikin horarwa na tsawon kwana biyar, wanda kuwa zai dasa ne akan kwarewar da mahalarta suke da ita kuma ya kirkira hanyar tuntubar juna da karawa juna ilimi, fahimta da kwarewa. Cikin littafin akwai babi-babi guda bakwai, kuma ko wane babi yana da bangaren da yayi dai-dai dashi daga littafin mai horarwa.

Shi wannan taron horarwar an tsara shi ne don mahalarta mutum 20-25, don haka ana bada shawara mai tsara taron horarwar da yayi kokarin chankowa daga kowanne bangare a tsakanin al’umma wurin zaben masu halartar taron.

**ROMMY MOM**

**Mukaddashiya ta Kasar Najeriya**
**Global Rights**
**May 2010,**

**HARUFFA MASU WAKILTAR SUNAYE**

**AU - African Union: Kungiya hadin gwiwar Kasashen Afurka.**

**AG - Attorney General: Kwamishinan Shari'a.**

**ADR - Alternatibe Dispute Resolution; Sulhu**

**CA - Court of Appeal: Kotun Daukaka kara.**

**CC - Criminal Code: Tsarin Dokoki da suka shafi laifuka na kudancin Najeriya.**

**CEDAW - Conbention on the Elimination of All Forms of Discrimination Against Women: Gwagwarmayar Kawarda Kowace irin Wari Ga Mata.**

**CRL - Child Rights Law: Dokar Kare 'yancin 'Ya'ya.**

**CFRN - Constitution of the Federal Republic of Nigeria: Kundin Tsarin Mulki Tarayyar Najeriya**

**CSOs - Cibil Society Organisations: Kungiyoyin Hadin Kan Ma'aikata.**

**FHR - Fundamental Human Rights: Hakkin Dan-adam na Matakin farko**

**HR - Human Right: 'Yancin Dan-adam.**

**HRC - Human Right Commission: Hukumar Kare Hakkin Dan-adam.**

**ICESCR - International Conbention on Economic, Social and Cultural Rights: Gwagwarmaya akan 'Yancin Dan-adam game da Tattalin Arziki, da Huldar da Jama'a da Al'adu ta Duniya.**

**ICCPR International Conbention on Cibil and Political: Gwagwarmayar Duniya akan 'Yancin dan-adam game da kasancewa dan dasa da na Siyasa.**

**LAC - Legal Aid Council: Majalisar Bada Taimakon Gaugawa a Harkokin Doka.**

**MCA - Matrimonial Causes Act: Dokokin Zaman Aure.**

**NA - National Assembly: Majalisar Kasa**

| | | | |
|---|---|---|---|
| **NHRC** | **-** | **Hukumar KARE Hakkin dan-adam kasa** | |
| **PC** | **-** | **Penal Code:** | **Tsarin Dokokin Laifuka ta Arewacin Najeriya.** |
| **SC** | **-** | **Supreme Court:** | **Kotun koli.** |
| **UK** | **-** | **United Kingdom:** | **Masarautar Turai.** |
| **UN** | **-** | **United Nations:** | **Majalisar Dinkin Duniya.** |

**JADAWALIN LITTATTAFAN DA AKA BINCIKA**

**Kundin Tsarin Mulkin Tarrayyar Najeriya**

**Tsarin Dokar Laifuffuka ta Kudancin Najeriya, Tsarin na 77, dokar kasa**

**Gwagwarmayar Kawar da kowace irin Wariya ga Mata**

**Matakan 'Yancin Dan-adam dana jama'a na Afurka**

**Hakkin Matan Afurka**

**Dokokin Zaman Aure 1970**

**Dokar Wasiyya 1837**

**Gyaran Dokar Wasiyya 1852**

**Al-Kur'ani Maigirma**

# BABI NA 1

## SANIN AIKIN DAN-AGAJIN ADALCI

Abu ne mai matukar mahimmanci, ita kanta tsarin shari'a ta zama mai samuwa ga marasa karfi, ta zama mai saukin samu kuma ta zama mai biyan bukata. Duk kan tsarin dokar 'yancin dan-adam bata da wata fa'ida idan ya kasance mai kudi kadai ke iya samun adalci, ko kuma idan hukunci ya samu jinkiri marasa dalili.

***NELSON MANDELA, 1994***

## GABATARWA

Samun adalci hakkin dan-adam ne wanda ya kamata kowa ya samu. Hana mutum adalci yana iya zama kara keta hakkin wannan mutum, kuma zalunci ne. Samun ayukan shari'a na kara yin wahala a mafi yawan wurare a kasar nan, musamman a yankuna na karkara; jahohin arewa ma ba baya ba. Mafi yawan matan arewacin Najeriya basu samun damar kaiwa ga adalci a lokacin da suke bukata. Rashin samun damar samun shawarwarin yadda za'a cimma adalci ga matan arewa nada alaka da dalilai da dama kamar:

- Ayyukan shari'a daga gurin lauyoyi yana da tsada, ta yadda matan karkara dake da karancin hanyoyin kudi basu iya biya

- Mafi yawan lauyoyi na zaune ne a manyan garuruwa ba karkara ba.

- Lauyoyin gwamnati wadanda aka tanada don taimakawa matalauta su samu adalci basu da isasshen tallafin kudi da ma'aikata don gudanar da aiki cikin nasara. Mafi yawa ofisoshinsu na manyan biranen jahohi, wanda hakan nasa abar wasu ban garori, musamman karkara ba tare da isasshen tallafi ba.

- A dai-daikun wuraren da mata kan samu damar kai kara kotu, sukan rude saboda rashin taushin harshen da ake amfani dashi a kotu; sannan kuma suma ma'aikatan kotun na ruda su.

- Ana kuma kange mata daga samun adalci da kuma samun shawarwari game da doka saboda wasu abubuwa na al'ada a cikin al'uman su.

Saboda wadannan dalilai ne al'amari yake tsananta a inda zalunci da keta hakkin dan-adam ga mata ke faruwa akai-kai, kuma babu wani mataki da ake dauka don magance hakan. Abune mai matukar mahimmanci a dauki mataki akan wannan dalubale ta hanyar inganta samar da adalci ta samar da agajin shari'a ga mutane marasa kariya, wanda a mafi yawan lokutta sune matan karkara.

## WANENE DAN AGAJIN ADALCI

Dan-agajin adalci shine mutumin da ke bayar da agajin gaugawa ga duk mutumin dake bukatar shawarwari gameda shari'a. Dan-agajin adalci ba lauya bane, kuma ba ya maye gurbin lauya a suna ko a aiki. Dan-agajin adalci shine wanda ke bayar da shawarwari masu sauki da taimako ga mutanen dake bukatar haka game da shari'a don taimaka masu

a matakin farko mafi kusanci wurin warware matsalolinsu na shari'a. Duk wanda ke iya karatu da rubutu a ko wane harshe na iya zama dan-agajin adalci idan ya samu horon da ya dace.

## MENENE AIKIN DAN-AGAJIN ADALCI

Wadannan na daga cikin aikin dan-agajin adalci:-

- Ilimantar da jama'a game da hakkokinsu na shari'a da yadda zasu samu adalci daga fannin shari'a
- Bayar da shawarwari masu sauki da taimakon jagoranci ga dai-daikun mutane da kungiyoyi don warware matsalolin su.
- Bayar da taimakon jagoranci game da yadda za'a shigar da al'amari gaban kuliya da kuma yadda za'a ansa.

## KIRAN SHARI'A

- Mika al'amari gaba zuwa ga wani mutum da ya dace ko lauya, ko wani ofishin gwamnati don taimaka ma mutanen dake fuskantar al'amarin shari'a game da matsalar gaban su.
- Taimaka ma mutanan dake fuskanta al'amarin shari'a wurin rubuta korafe korafe, ko ja, ko yarjejeniya ko rantsuwa kotu don warware matsalar dake gabansu.
- Sasanci ko zamowa mai sassauci (a takaitattun wurare, kuma a inda ya dace kadai) don taimakama masu fuskantar al'amarin shari'a wurin warware matsalar gabansu.
- Raka masu fuskantar shari'a zuwa kotu don basu kwarin gwiwa, taimaka masu da kuma nuna masu yadda al'amari yake game da irin harshen kotu da matakan gudanarwa na kotu.

Sau da dama dan-agajin adalci kanyi aiki da lauyoyi, musamman irin lauyan da ake kira "Prono-bono lawyers" (wato lauyoyin da ke aiki kyauta) don taimaka ma mutane wurin warware matsaloli masu rikitarwa a harkar shari'a. Lauyoyi ma sukan bada taimakon jagoranci da shawara lokaci-zuwa-lokaci game da mafi dacewar hanyar da za'a tunkari matsala mai rikitarwa.

**DABI'UN DAN AGAJIN ADALCI NA KWARAI**

a. Wajibine dan-agaji adalci na kwarai ya zama ya waye da doka, yadda take a rubuce da kuma yadda ake aiki da ita.

b. wajibi dan-agajin adalci na kwarai ya zama mai kyawawan halaye, wanda ake ganin kimarshi a cikin al'umma.

c. Wajibine dan-agajin adalci ya sadaukar da kai wurin tallafawa mutanen da ke neman adalci.

d. Wajibine dan-agajin adalci ya iya Magana

e. Wajibine dan-agajin adalci ya zama mai jin-kai

f. Wajibine dan-agajin adalci ya zama mai kamun kai, kuma ya kiyaye sirrorin da aka baiyana mashi

**DABARUN AIKI DA SUKA WAJABA DAN-AGAJIN ADALCI YA KWARE DASU**

- **DABARUN TATTAUNAWA:-**
  Akwai bukatar dan-agajin adalci ya ware wurin tattaunawa da mutane don gudanar da aiki cikin nasara. Wannan zai taimaka wurin samun kyakkyawar fahimtar matsalar kowane mutum da kuma al'amuran dake kewaye da wannan matsala. A yayin tattaunawa da mutumin da ke da neman agajin adalci, yana da matukar mahimmanci kasa shi ya kwantar da hankali, ya saki jiki yayi Magana. Mutumin da yazo gurinka yana bukatar taimakonka ne, don haka ka tabbatar babu dalilin da zai sa ya rude. Ka tabbatar cewa mutumin da ke neman shawararka ya fahimci matsayinka na dan-agajin adalci. Wadannan abubuwan zasu taimaka maka gurin gudanar da tattaunawa:-

  - Ka nuna kasan kimar mutum kuma ka girmama shi.

  - Ka tabbatar da ingancin yanayi da natsuwar rai ga mutumin da kake tattaunawa dashi.

  - Ka zamo a natse, ka mayarda hakali ayayin da ake tattaunawa.

  - Ka rika sauraro da fahimtar bayanin mutum ayayin tattaunawar don tabbatar wa mutumin cewa kana fahimtar matsalarshi.

  - Ka bayyanawa mutum dalili da mahimmancin tattaunawar.

  - Kada kazamo mai kokarin yanke wa mutum hukuncin yin dai-dai ko rashin yin dai-dai, ko karyatawa ko nuna rashin gamsuwa da halayyar mutum a yayin da kake tattauna matsalarshi.

- Ka biye bayan jawabai da tambayar karin bayani.

- Kayi tambayar da bata hana mutum damar bayani ba, ka guji yin tambayar da ke nuna cewa abinda ka fahimta shi kadaine gaskiya ba abinda mutum ke kokarin nunawa ba.

- Kayi kokarin yiwa mutum ta kaitaccen bayanin abinda ka fahimta daga bayaninshi don kawar da kuskuren fahimta

- **DABARUN TAIMAKON JAGORANCI DA SASANCI**
  A matsayinka na dan-agajin adalci, dole ne ka bayar da taimakon jagoranci wani lokaci ma har ka sasanci a cikin al'amarin da aka kawo gareka. Ana sasanci (ayi ruwa ayi tsaki) ne a wuraren da bai kyautu a kyale wani hakki na wata mace haka nan ba kadai, ban da wuraren daba haka al'amarin yake ba. (ya kamata ka duba kwatancen da akayi a cikin babi mai zuwa gameda wurin da ya kamata da wurin da bai kamata a shiga ayi ruwa ayi tsaki ba). Gaskiyar al'amari shine mafi yawan harkallolin da zaka ci karo dasu a matsayinka na dan-agajin adalci ba zasu kai kotu ba, sabo da tsawon lokaci da ake dauka a kotu kafin a warware matsala da kuma wahalar dake tattare da jan shari'a. Mafi yawan mutane suna bukatar maslaha mai sauri, kuma mai saukin tsada kuma mai biyan bukata a cikin al'amarin su. Sabo da haka mutane da yawa zasu bukace ka da ka basu taimakon shawara, kuma ka sasanci a cikin rikicin su. An tanaji isasshen bayani game da taimakon jagoranci da sasanci a babi na gaba.

- **MIKA AL'AMARIN RIKICI GABA**
  A matsayinka na dan-agajin adalci, ba zai yiwa ka iya warware kowace irin matsala tun daga farko har karshe da kan ka ba. Mafi yawan lokaci zaka tura al'amarin mutum zuwa ga wani lauya ko wani wanda zai iya bada maslaha irin ta kwararren masani. Baya ga lauyoyi, kana iya tura mutum zuwa ga hukumar kare hakkin dan-adam ta kasa ko ga kungiyoyin kare hakkin dan-adam, ko ga ofisoshi ko ma'aikatan gwamnati koga hukumomin da suka dace da sauransu. Don haka ya kamata ka waye da irin aiyukansu da kuma yadda ake samun aiyukan nasu. Akwai bukatar ka ajiye bayanan yadda zaka iya tuntubarsu, in zai yiwuma ka kirkiri wata 'yar alaka dasu, yadda zaka samu damar tunkarar su idan matsala ta taso. Zaka bukaci rubuta wasikar mika al'amari zuwa garesu, kuma ka tabbatar ka bi kadin matakin da aka dauka.

- **RUBUTUN WASIKA**
  Ana bukatar dan-agajin adalci yakware wajen rubuce-rubuce don samun nasarar aiki. So da dama za'a bukaci ka rubuta wasikar korafi ko ja don shigar da harkallar da suka kawo.

  A yayin da kake rubuta wasika, ka sa wadannan abubuwa a zuciyarka:

- Kayi wasikarka ta zamo mai saukin fahimta kuma ka takaita rubutunka bakin gwargwado.

- Ka tabbatar ka rubuta adireshin wanda kake rubuta ma wasikar dai-dai.
- Ka tabbatar ka bayyana matsayin wasikarka filla-filla.
- Kayi bayanin bukatarka ga wanda kake rubuta ma wasikar flla-filla.
- Ka rike kwanan watan dake jikin wasikar
- Kada ka manta ka sa hannu a karshen wasikar. A wasu wuraren, wanda harkallar ta shafa shima sai ya sa hannu. Kai ne zaka tantance inda ya kamata da inda bai Zama dole mai harkalla ya sa hannu ba a cikin harkallolin da ka ke aiki da su yau da gobe.
- Ka aika da kwafin wasikar zuwa ga masu ruwa da tsaki da kuma duk Wanda al'amarin ya shafa don su samu masaniya.
- Ka nemi amsa daga mutumin da ka aikama wasikar.
- Ka tabbatar wasikar ta isa akan kari kuma kayi bakin iya kokari ka samu shaidar isarta (Misali: Sa hannun mai karba).

  An tanaji misalin yadda ake rubuta wasika a karshen littafin nan.

- **TATTARAWA DA MIKA BAYANAI**
  Dole ne dan-agajin adalci yakware wurin nemowa da adana bayanan mutane da shiga harkallarsu. Dole ne dan-agajin adalci ya sa ido kuma ya tattara bayanin daya shafi ko wanene mutumin, kwanan wata da lokacin haduwa, shawarar da aka bayar, matakan da ake bi, da kuma yadda aka mika al'amari gaba, idan anyi hakan. Dole ne dan-agajin adalci ya sa ido kuma ya tattara bayanan duk yadda al'amari ya kasance game da harkallar dake gabanshi ko don amfanin gaba. Ya kamata a takaita kuma a saukaka bayanan da aka tattara don saukin fahimta. An tanaji misalin yadda za'a rubuta baya nan a karshen wannan littafi.

# BABI NA 2

## DABARUN BADA TAIMAKON SHAWARA DA SASANCI

**YADDA AKE BADA TAIMAKON SHAWARA:**
Kamar yadda akai bayani a baya , aikin bayar da taimakon shawara Kanwa uwar gamin a cikin aikinka na dan-agajin adalci, don haka wajibi ne kayi tattalin hanyoyin kwarewa da wannan bangare na aikinka. Mutane zasu zo maka ne da zummar samun shawararka akan abinda ya kamata suyi dangane da matsalar su. Kuma su nemi taimakonka wurin yin hakan. Muhimmin aikinka a yayin bada taimakon shawara shine taimaka ma mutum ya fahimci matsayin al'amarinshi a wurin doka da kuma hanyoyin da zai iya bi don warware matsalar.

Kafin ka samu damar bada shawara fitar maslaha a cikin al'amarin mutum, dole sai ka samu ingantacciyar fahimtar gaskiyar al'amarinsu da kuma matakan da aka riga aka dauka.

**DON BADA TAIMAKON SHAWARA MAI FA'IDA, SAI KA SAMU:**
Fahimtar dokokin da suka shafi al'amarin mutumin da kuma hanyoyin dake akwai wurin bin kadin matsalar.

Iya nazarin matsala dalla-dalla tare da danganta ta da ilminka na shari'a shi zai baka damar fito da hanyoyi warware matsalar. Haka nan kuma:

- Kyakkyawar shimfidar fuska ga mutum da iya bada kwarin gwiwa.
- Iya hulda da al'amuran sirri da dabi'un kwararru.
- Iya Magana; Iya sauraren bayani, fahimtar canjin fuska da iya bayani da yaren mutumin.

A yayin bada taimakon shawara, ka rike a ranka cewa yana da muhimmanci kada kayi alkawarin daba zaka iya cikawa ba, ko ka bada shawarar da baka da tabbas a kanta. Idan kaga ba zaka iya warware matsala ba to ka mika al'amari gaba zuwa wurin lauya ko kuma wata hukuma da ta dace.

**Matakan bada Taimakon Shawara**

**Misalin nan da zai biyo baya zai baka manuniya game da yadda ake gudanar da aikin bada taimakon shawara:**

- Idan mutum ya tunkare ka da neman shawara a harkar sharia.
- Sai ka cika mashi fom wanda a ciki zaka rubuta bayanan shi.
- Mutumin zai baka labarin matsalar shi da yaren da yake ji kuma da irin nashi salon Magana.

- Sai kayi mashi tambayoyi neman karin bayani don tantance manufa, kuma ka kara zurfafa binciken don ka gano wasu abubuwa masu dangataka da matsalar, wadanda bai fada ba, kuma wadanda zasu iya taimakawa wurin warware matsalar.

- Ka sanar da mutuminka matsayin al'amarin shi a idon shari'a. Idan baka da tabbas akan abinda doka zata iya yi game da wannan al'amari, sai ka gaya ma mutuminka ya tafi ya dawo a wani lokaci na gaba kai kuma sai ka tuntubi lauya don Karin bayani.
- Daga nan sai ka sanar dashi mataki na gaba.

| Wurin da zaka iya shiga kayi-ruwa-kayi-tsaki. | Wurin da ba zaka shiga kayi-ruwa-kayi-tsaki ba. |
|---|---|
| | A yayin da aka keta hakkin farko na mutum |
| Idan akwai yiwuwar ci gaba da hulda tsakanin ma su rikici. | A wurin da masu rikici basu da bukatar sasanta takaddamarsu. |
| A yayin da mai bin hakki ba shi da lokaci ko kudin jan shari'a. | A yayin da aka aikata laifi, misali; Fyade, Kisa, cin zarafi, gallazawa mata ko kananan yara, gallazawa a wurin saduwa ko tsakanin jinsi da sauransu. |
| A yayin da mai bin hakki yafi son a sirranta al'amari | A yayin da rayuwar mai bin hakkin ke fuskantar barazana. |
| | A yayin da al'amarin rikicin ya shafi fassara doka ne zalla. |

**DABARUN AIKI WURIN SASANCI**

- Wajibine mai sasanci ya zama ya iya Magana.

- Wajibine mai sasanci ya zama ya iya zama da mutane.

- Wajibine mai sasanci ya fahimci tsarin tunanin mutane

**DOKOKIN AIKI GA MAI SASANCI**

i. Ka tuna cewa, sasanci ba hanyar gano laifi ko rashin laifibane, hanya ce dai ta sasanci.

ii. Nauyin dake wuyanka a matsayin mai sasanci bai kai na bada mafita kai tsaye ga harkallar dake tsakanin masu rikici ba, kai dai naka shine kokarin share masu fagen da zasu iya samun maslaha a tsakaninsu.

iii. Ka kasance mai sanin kimar mutanen da kake hulda dasu kuma kaba kowa dama kwatankwacin wacce kaba abokin harkallar shi. Ka saurari bayanin kowa dai-dai da dai-dai.

iv. Dole ne ka kawar da ra'ayinka da son-zuciya daga cikin hidimarka ta mai sasanci.


v. Kayi kyakkawan sauraro da fahimta don gano abinda masu harkalla suke so. Wani lokaci, bangaren da ke Jin tsoron kaye sukan manne ma mataki mafi tsauri ko da kuwa suna da ra'ayin sasanci. To ka saurari labarin kowa dai-dai gwargwado, ka ba kowa cikakkar dama da lokaci suyi bayanin damuwarsu.

vi. Idan ka gana a sirrance da daya daga cikin bangarorin da ke harkalla, to ka maimaita haka da daya dangaren.

vii. Ka dauki dan gajeren lokaci ku huta baki dayanku, musamman a lokacin da kaga bangarorin sun dauki zafi. Yin hakan zai bada damar su huce sannan sai ka dawo bakin aiki. Haka kuma daukar hutun zai baku damar yin nazarin abubuwan da aka riga aka tattauna akai.

**MATAKAN SASANCI**

Duk da yake dai tafarkin sasanci nada salo iri-iri, akwai matakan da basa sauyawa a kowane irin salo. Haka kuma ba lallai bane abi matakan daki-daki, ko sai an gama wani kafin a shiga wani, a'a yanayi ke bada matakin da za'a shiga, kuma shi ke bada yiyuwar komawa wani mataki bayan an barshi, ko ketare wani mataki a shiga wani.




**SHIRYAWA**

A matakin shiryawa, zaka kintsa kanka dan sasanci wurin sasanci ta hanyar bin matakan da za'a samu cimma matsayar da duk bangarorin dake rikicin zasu gamsu da ita. Idan zai yiwu, to a samu rubuttar shaidar da zata tabbatar da amincewar bangarorin, da kwanan

wata, da wurin da zakayi wannan zaman sasanci. Sannan kuma ka bayyana ko su wanene kake shirin zaman da su da kuma sauran masu halartar wannan zama. Kayi bayanin irin takardu da litattafan da keda nasaba da tattaunawar, sannan ka fayyace yiwuwar bukatar wani mai sasanci a wurin wannan sasanci.

**BUDEWA**

Idan kazo bude wannan taron sasanci sai ka yi wa mahalarta taron maraba. Kuma kaba kowa damar gabatar da kanshi tare da bayyana matsayinsu a cikin taron.

Sai kuma ka gabatar da kanka (idan kuma akwai wani mai shiga tsakinin, shima ka gabatar dashi). Kayi bayanin matsayinka na mai sasanci ga bangarorin. Misali "Sunana Amina Mohammed kuma ni mai sasanci ce."

Kayi karin haske akan matsayin aikinka na sasanci, kuma ka sanar da su matakan wannan taro. Misali: Ni ba alkakali bane ba kuma mai yanke hukunci bane. Aiki na shine in share maku fage ta yadda zaku iya sasanta junanku game da rikicin dake tsakaninku. Ya kamata mu fara da shimfida sharuddan da zamu yi aiki dasu a cikin wannan taro, tare da tabbatar da cewa sharuddan sunyi dai-dai da ra'ayin kowanenmu. Bayan mun gama da wannan, sai ko wane bangare yayi bayanin abinda ke ranshi. Bayan kowa yayi bayani, tana yiwuwa in bukaci tattaunawa a sirrance da ko wane bangare ko kuma mu hadu gaba daya mu tattauna hanya mafi dacewa wurin warware wannan rikici. Bayan mun gama wannan, zamu yi waiwaye adon tafiya akan duk wata yarjejeniya da muka cimmawa, da kuma sharuddan da muka gindaya sannan sai muyi a rubuce. Shin kowa ya gamsu da wannan bayani?"

**SHIMFIDA SHARUDDAN TARO**

Mutane da dama sukan gaza rike fushinsu idan wata harkalla ta hadosu da wani. Wannan kuwa ya kara mayar da hannun agogo baya tare da hana ruwa gudu a wurin sasanci. Don guje ma irin hakan tare da tabbatar da samun ingantaccen yanayi a yayin sasancin, yana da muhimmanci a shimfida sharuddan a lokacin da za'a fara sasanci. Sharuddan suna iya bambanta dai-dai da yanayin harkalllar da ake fuskanta. Sharuddan da akafi amfani dasu yau da kullum sune: banda datse hanzari, banda kiran mutum da sunayen batanci, banda zagi, da sauran su.

**TABBATAR DA RUFIN ASIRI**

A tabbatarwa da duk bangarorin da cewa duk abinda aka tattauna ko kuma akayi a wurin wannan sasancin sirri ne. Don haka ba za'a yada ma duniya ba ko ayi amfani dashi a kotu. Sannan kuma dole ne duka bangarorin su tabbatar sun amince da wannan sharadi. Tabbatar da rufin asiri zai taimaka ma kokari a sasancin, sabo da kowane bangare zai saki jiki ya fadi abinda ke ranshi ba tare tsoron tonon silili ba ko tsoron a kama mutum da maganarshi.

**TABBATAR DA IKON ZARTASWAR MAHALARTA SASANCI**

Duk kokarinka wurin sasancin na iya zama tsantsar bata lokaci idan har mahalarta taron sasancin basu da ikon tabbatar da sasanci akan rikicin da ke akwai. Babu kamar idan

daya daga cikin bangarorin na wakiltar gwamnati ne, ko wata hukuma, ko wata ma'aikata, ko wata kungiya, ko wani mutum. Misali, idan wani banki ya aiko ma'aikacin shi mai matsayin mataimaki a aikin ofis, ya zo don wakiltar bankin akan rikicin bashi, to mawuyaci ne bankin ya bashi cikakken ikon warware rikicin. Don haka, ko Manaja ne yazo, to ya kamata a tabbatar in yana da cikakken ikon warware rikicin.

**BADA BAHASI**

A gayyaci ko wane bangare ya fadi ta bakinshi, kuma a ba kowa isassar dama da lokaci. A saurari kowanne da kunnen basira tare da karfafa gwiwar kowa yayi bayani irin yadda ya iya yin bayani. Ayi tambaya don karin haske akan kalamai masu harshen damo, da kuma samun karin bayani. (a guji katse hanzari duk da haka).

Sai ayi ma duk wanda ya gama bayani godiya, ayi takaitaccen bayanin abin da aka fahimta daga bayanin mai Magana, a tambaye shi idan fahimtar tayi dai-dai. A tambayi mai Magana idan akwai wani kari da zaiyi akan bayaninshi. Wannan ne zai baka damar samun kyakkyawar fahimtar yanayi yadda kowane bangare ke kallon al'marin.

Sai ka mai maita haka da dayan bangaren.

**FAHIMTAR MATSALA**

Wanna zangon shine zangon da za'a duba irin hanyoyin da ke akwai wadan da za'a iya amfani dasu wurin warware rikicin. Ya kamata a lura cewa sau da dama, ainifin bukatar bangarorin da kuma ra'ayoyinsu sukan sha bam-ban da abinda suka bayyana da bakinsu. Don haka dole ne ka gano kuma kayi amfani da ainifin bukatarsu da kuma ra'ayoyinsu. Dole ne ka karfafa masu gwiwa suyi amfani da dama mafi dacewa wurin.

**BINCIKEN MATSALA**

Ka tattara bayanai masu dangantaka da juna daga bayanan bangarorin wuri guda. Su bangarorin da kansu ne zasu kirkira sharuddan daidaitawa a tsakaninsu. Ka jinjina nauyin ko wace Magana kuma ka fayyace ta, kana mai auna muhimmanci da rashin muhimmancin ta. Ka karfafa masu gwiwa akan su gyara, kuma su sassauta don a samu mafita.

Ka tabbata da cewa sharaddin sasancin su ya hade duk abinda ake rikicin a kanshi. Kuma ka tabbatar sharuddan a bayyane suke ba masu harshen damo ba. Sannan ka tabbatar sharuddan masu yiwuwa ne. Kana iya yin aiki da wannan a zancen:- Mai yiwuwa, Mai biyan bukata, Mai karbuwa, Na dun-dun-dun.

**MASLAHA**

Da zaran duk bangarorin suka cimma kwakkwarar matsaya, sai ka rubuta sharuddan yarjejeniyar da suka cimmawa a matsayin alkawarin sasanci wanda kowane bangarare zai sama hannu.

To menene matsayin sasancin da aka samu sabani akan wasu daga cikin sharuddan yarje jeniya? ko hakan na iya rusa sasancin baki daya? A'a ba haka bane. bangarorin na iya sasanta sauran sharuddan ta hanyar shari'a gaban kuliya, ko duk ta hanyar da suka gamsu da ita

# BABI NA 3

## TSARIN SHARI'AR NAJERIYA

Doka wani tsari ne na hukunce-hukunce da aka shimfida don dai-daita huddodin mu da juna a cikin al'umma, kuma ta zama ma'aunin dangantakar mu da al'umarmu baki daya. Shi tsarin doka ya lullube duk wani dan kasa, sannan rashin biyayya ga doka na kawo rudani da rikici a cikin al'umma. Ana tabbatar da bin doka ta hanyar amfani da wasu hukumomi, wadanda gwamnati ta ba hurumin yin hakan.

Tsawon lokaci, kowace al'umma tana tsara nata tsarin doka ne don 'ya'yan wannan al'umma su amfana da wannan tsari. Tsarin doka na da matukar amfani ga wanzuwar ko wace al'umma. Da ita ake amfani a tabbatar da tsarin da kuma zaman lafiya. Sannan kuma ana tabbatar da ganin duk wanda ya sabama doka to an hukunta shi.  Mafi yawan al'ummomi suna amfani da doka a matsayin ginshikin samun cigaba.

Don yin tasiri a matsayin dan-agajin adalci yana da kyau ka saba da tsarin shari'ar Najeriya, musamman tsarin shari'ar da ake amfani dashi a arewacin Najeriya.  Ta wannan hanyar ne kadai zaka samu damar ilimantarwa da bada shawara mai amfani ga wanda kake hulda dashi game da matsayin al'amarin su ga doka da kuma mafi kyawun hanyar data kamata abi game da al'amarin. Saboda haka, zamu tabo kashin ukun dake akwai na tsarin dokar da ke aiki a arewacin Najeriya; da kuma hanyoyin da ake bi wurin kirkira dokoki a arewacin Najeriya, da kuma yadda ake shigar da kara a kotu, da yadda ake amsa kiran shari'a da kuma yadda ake tunkarar al'amarin jami'an tsaro, musamman ma 'yan sanda.

## TSARIN DOKAR DA YA SHAFI JAMA'A KADAI

Don kokarin fahimtar ko mecece doka, ya kamata mu kalli al'amarin doka ta fuskar dokar tsakanin gwamnati da jama'a, kuma dokar  tsakanin jama'a zalla. Dokar tsakanin gwamnati da jama'a wato Public Law a turance itace tsarin dokar da yake hukunci a tsakanin mutane dai-dai ku da gwamnati.  Tsarin dokar jama'a zalla kuwa, wato Pribate Law a turance shine tsarin  dokar dake hukunci tsakanin dai-dai kun mutane.  Misali: tana hukunci akan kwangila tsakanin mutane dai-dai ku,  dokar  kwadago, dokar iyali, dokar aure, dokar gado, da sauransu.

## DOKAR DA TA SHAFI LAIFUFFUKA

Dokar da ta shafi laifuffuka wato Criminal Law a turance, wani bangare ne na dokar gwamnati da mutane wadda ta shafi laifi da hukunci. Daga hurumin dokar ne ake gudanar da binciken laifi, da kamo wanda ake zargi, da tuhumar shi, da kama shi da laifi. Akwai bambanci tsakanin saba ma kyakkawar dabi'a da kuma aikata laifi. Ba za'a iya kama mutum da laifi akan yin wani abu ba har sai in doka ta tabbatar da kasancewar wannan abu laifi a dai-dai lokacin da ya aikata shi. Nauyin tabbatar ma mai laifi da laifinshi yana kan shari'a, kuma dole ne sai an tabbatar da laifin tabbatarwa ta yankan shakku. Ana yanke hukuncin ladabtarwa don a inganta biyayya ga doka. Ladabtarwa kuwa na daukar salo iri-iri, wadanda akafi sani sune:-tara, yari, da sauransu.  Hukuncin laifuka

mai suna Criminal Code (cc) a turance shine tsarin da ake amfani dashi a kudu arewa kuwa na amfani da tsarin hukunci da ake kira Penal Code (PC) aturance.

## DOKAR NEMAN HAKKI

Wannan tsarin doka da aka fi sani da suna Cibil Law a turance wani reshe ne na dokar jama'a da gwamnati wanda ya danganci yima juna laifi tsakanin dai-daikun mutane. Ire-iren laifukkan da akanyi ma juna a wannan tsari kan dauki hukunci da biyan diyya, da biyan barna da sauransu.  Ana yin hukunci da irin wannan dokar ne don mutane su kwaci hakkinsu a shari'ance kuma su samu diyya bisa ga barnar da akayi masu ko asarar da aka jawo masu. Saboda haka, duk wanda ke neman diyya saboda wani laifi da wani yayi mashi yana iya shigar da kara akan wannan doka. Misalin irin wannan laifi shine: **s**aba yarjejeniyar kwangila, rashin biyan albashi, rikici akan fili ko gona da sauransu. Shi kuwa mutumin da aka ci zarafinshi, ko aka doke shi, ko fyade, ko fashi da makami, to kasa zaka shigar da kara akan dokar laifuffuka don ta bada kariya ga mai gaskiya kuma ta hukunta mai laifi.

## TSARIN DOKA MAI FUSKA UKU

Kasar Najeriya tana tafiyar da mulki ne akan tsarin mulki na tarayya.  A dalilin haka muna da tsarin dokar gwamnatin tarayya da kuma na jihohi. A takaice dai Najeriya na tafiyar da tsarin shari'a na tarayya da na jiha a tare. Kusan ko wace jiha ta arewacin Najeriya tana tsarin shari'a kashi uku ne kamar haka:-

- Dokar game-gari
- Dokar tsarin gargajiya/Al'ada
- Dokar Shari'ar Musulunci

Ko wane daga cikin wadannan na da kotu ta musamman da kuma hanyoyin shimfida doka.

## HANYOYIN SHIMFIDA DOKA A NAJERIYA

## DOKA GAME-GARI

Ita dokar game-gari itace dokar da aka gada daga turawan Ingila. Kasancewar Najeriya kasar da ta taba zama karkashin mulkin mallakar Ingila, ta ari dokokin Ingila na game gari, har ta kai ga cewa mafi yawan dokokin da ake aiki dasu a yanzu, sun samo asali ne daga dokokin mulkin mallaka wato gabanin shekarar 1960.

## GABATA A SHARI'A

Daya daga cikin bangarorin tsarin dokar da aka aro daga Ingila shine amfani da tsarin dake bada damar cewa hukuncin da kotun sama ta yanke, ya zama doka ga shari'o'in wanna kotun da kuma kotun dake kasan ta, yin haka ya samar da wani jerin dokoki daga hukunce hukunce.

## TSARIN MULKI

Tsarin mulkin Najeriya na (1999) shine mafi girma a tsarin doka a Najeriya. Duk dokar da ta saba mashi to nan take tazama haramtatta. Shi tsarin mulkin wani jerin dokoki ne wanda ke hukunci a cikin gwamnati.

A matsayin dan agajin adalci, sashen tsarin mulkin Najeriya da yafi shafar sha'anin ka shine Babi na 4, wanda ke dunshe da tanadin gwamnati akan kare hakkin dan-adam da kuma hukunta duk wanda ya keta wannan hakki. Zamu kara taba wannan maganar sosai nan gaba.

**DOKAR MAJALISAR KASA**

Dokokin majalisar Najeriya wasu dokoki ne da hukunce-hukunce da zartarwa wanda 'yan majalisar kasa sukeyi. Kamar yadda tsarin mulki ya tanada, 'yan majalisar kasa dana ko wace jiha suna iya zartar da doka. Majalisar kasa tana yin doka ta tarayya. Ita kuwa majalisar jiha tana yin dokar da ta shafi jiharta. Wannan na nuna kenan akwai dokokin jiha akwai na tarayya. Dokar jiha kuwa tana aikine a jihar da ta shafa. Ita kuwa dokar tarayya ta hade kasa ne baki daya. Ana yin hukunci da dokokin majalisa a kotun gwamnati.

**DOKAR GARGAJIYA/AL'ADA**

Dokar al'ada ko kuma ace doka 'yar gida itace dokar da aka tsatso daga wata al'ada wadda mutanen wata al'umma ke biyayya gareta. Sau da dama dokar ta danganta da kabila da kananan bangarorin kabila. Haka na nuna irin tsarin rayuwarsu da kuma tsarin al'adarsu. A Najeriya, dokokin al'ada ba rubutattu bane, masu sanyuwune dai-dai da zamani kamar yadda al'adun mutane ke sanya wa. Ana hukunci da dokokin al'ada a kotunan gargajiya, da kotuna al'umma wanda bana gwamnati ba. Dokokin da akafi hukunci dasu daga cikin dokokin al'ada sune:- hukunci tsakanin mutane, gado, auren gargajiya, saki, da kuma ikon amfani da filaye.

Abin lura anan shine su kotunan al'ada ba su yanke hukunci da dokar da ta sabama adalci da gaskiya ba.

**SHARI'AR MUSULUNCI**

Ita shari'ar musulunci, za'a iya kiranta da shari'ar al'ada ta musulunci. Kuma itace take hukunci akan tsarin rayuwar musulmi. A'inda tasha bam-ban da dokar al'ada shine ita dokar shari'ar musulunci rubutattar dokace. Ana tsatso dokokin ne daga Alkur'ani mai girma da kuma koyarwar Annabi Muhammad(S.A.W). A wasu al'ummomin, shari'ar musulunci ta zama itace doka 'yar gida. Kusan duk jihohin arewa suna da kotunan shari'ar musulunci wadanda keyin hukunci tsakanin mutane. A dangane da al'amarin shari'ar laifuka kuwa, jihohi 12 ne suka rungumi shari'ar musulunci don hukunci akan laifuka don haka dokar laifuka ta kunshi shari'ar musulunci a matsayin hanyar shimfida doka. Kuma hakan ya fadada hurumin shari'ar musulunci daga matsayin hukunci tsakanin mutane dai-daiku zuwa hukunci akan laifuka.

**YARJEJENIYA DA DOKOKI NA KASA DA KASA DA YANKUNA**


Wadannan wasu dokoki ne da majalisar dinkin duniya tayi ko kuma wadanda kungiyar gamayyar Afurka, ko kungiyar tattalin arzikin al'umar yammacin Afurka (ECOWAS) tayi a matakin yanki. Gwamnati ita ke da nauyin amincewa da kuma sa hannu akan yarjejeniyar kasa da kasa kuma tana iya zama dokar kasa bayan an amince kuma an sa

hannu akanta. Irin wadannan yarjejeniya kan zama doka a Najeriya idan aka mayar dasu ‘yan gida. Sai dai Kash, mafi yawa daga cikin yarjejeniyar kasashen duniya na baya bayan nan, irin su “yunkurin duniya akan kawar da ko wane irin bambanci ga mata da kuma “tsare-tsaren hakkokin matan arewa” basu kai ga zama yan gida ba a Najeriya. Amma duk da haka, yarjejeniyar “Tsarin Afurka akan ‘yancin dan-adam da na jama’a” ta zama ‘yar gida kuma ta zama dokar Najeriya.

## TSARIN KOTUNAN NAJERIYA

### Yin shari’a akan

Ana iya kasafta kotunan arewacin Najeriya zuwa kotunan gwamnati da wadanda ba na gwamnati ba. Kotunan gwamnati sune kotunan da gwamnati ta kirkira kuma take tafiyar dasu. Su kuwa kotunan da bana gwamnati ba sune kotunan da al umma ta kirkira.




Tsarin Kotunan gwamnati ya kunshi kotunan da gwamnati ta kirkiro. A cikin wannan tsari, mafi yawan harkallar da zata zo maka za’a warwaresu ne a kananan kotuna da ke cikin wannan jerin kotunan. Kotunan sun kunshi:

## KOTUN YANKI, KOTUN SHARI’AR MUSULUNCI DA KOTUN AL’ADA

Kotunan yanki a Najeriya, kananan kotuna ne, kwatankwacin karamar kotun majistire. Suna da karancin hurumi. Suna yin shari’ar saki a tsarin dokar da ta al’ada, da hakkin rikon da a tsarin dokar al’ada. A jihar da babu kotun shari’ar musulunci, to sai kotun yanki ta kwantanta yin shari’a akan harkallar da ta shafi shari’ar musulunci, da suka danganci aure, saki, rikon ‘ya’ya da gado. Kotun gargajiya ita ke yin hukuncin akan harkallar da ta shaafi dokar al’ada. Kotunan shari’ar musulunci sune ke yin hukunci akan al’amuran daya shafi shari’ar musulunci tsakanin mutane dai-daikunsu sannan kuma tana da hurumin wasu daga cikin shari’o’in laifuffuka ga musulmi kadai. Duk da yake dai ita

kotun shari'ar musulunci bata bisa tsarin gwamnati kamar Babbar kotu, duk wanda keda harkalla cikin ta na iya daukar lauya don ya wakilce shi.

Wannan 'yancin ya samu kariya ne daga kundin tsarin mulki. Mafi yawan harkallar da ake kaiwa wannan kotu ta shafi tsakanin dai-daikun mutane ne. Misalin dokar iyali ta al'ada ko ta addinin musulunci, irin ta saki, hakki bayan saki, da kuma laifuffukan da ke dauke da horo a cikin shari'ar musulunci.

## BABBAR KOTUN YANKI, BABBAR KOTUN SHARI'A DA BABBAR KOTUN AL'ADA

Su wadannan kotunan suna iya yin hukunci akan laifuffuka da kuma shari'ar mutane ta neman hakki a bakin iyakar huruminta. Kuma ana iya daukaka wa zuwa ga wadannan kotuna daga kotunan yanki, da kotunan shari'ar musulunci da kuma kotunan al'ada.

## KOTUN MAJISTIRE

Ita kotun jiha ce wadda dokokin jiha suka kirkiro. Mafi yawa tana sauraren harkallar bin hakki da harkallar aikata laifi. Ta sha bamban da kotun shari'ar musulunci a huruminta domin kuwa ita tana aiki ne da dokokin majalisa ba dokar musulunci ba. Hurumin kotun majistire shima takaitacce ne kuma ya danganta da matsayin kotuna da kuma alal-misali yawan kudin da ke cikin harkallar.

## KOTUN DAUKAKA KARA NA SHARI'AR MUSULUNCI

Wannan kotu tana da hurumi amsa karar da aka daukaka da kuma hurumin sa ido akan kotun shari'ar musulunci. Harkallolin kotun sun hada da abubuwan da suka shafi hukunce-hukuncen shari'ar musulunci. Tana saurare tare da binciken karar da aka daukaka daga babbar kotun shari'ar musulunci, da kuma kotun yanki akan harkallar neman hakki da ta laifi. Sannan kuma tana sa ido tare da bada umarni ga kotunan shari'ar musulunci. Kotun tana da hurumi ne a yayin da duk bangarorin da ke shari'ar musulmaine, kuma da kansu suka amince ayi masu shari'a da hukuncin musulunci. Ko a wannan kotu ta shari'ar musulunci, lauyoyi na da 'yancin a saurare su.

## BABBAR KOTUN JIHA

Ita wannan kotu tana hurumi mafi fadi, kuma tana hukunci akan harkallar neman hakki da ta laifi. Sannan kuma tana iya sauraren daukaka kaara daga kotun majistire. Babu wanda ke da izinin wakiltar mutum a gaban wannan kotu sai kwararen lauya.

## BABBAR KOTUN TARAYYA

Ita wannan kotu tana da matsayi dai-dai da na babbar kotun jiha, amma kuma tana da wasu hurumomi da suka sha bam-ban, misalin al'amuran da suka shafi karbar rabanu, da harajin gwamnatin tarayya daga hannun kamfanoni, da kudaden shige-da-fice na kasa, da rikici tsakanin bankuna, da sha'anin zama dan kasa, da sauransu.

**KOTUN DAUKAKA KARA**

Ita wannan kotu tana da hurumin sauraren karar da aka daukaka daga babbar kotun jiha da ta tarayya, da kotun daukaka karar shari'ar musulunci, da kotun daukaka dara ta al'ada da kuma hukuncin da aka yanke a kotun soja ko kuma kotunan musamman kamar yadda dokar majalisar kasa ta tanada. Haka kuma tana da hurumin yanke hukunci akan ingancin zaben mutumin da aka zaba a matsayin shugaban dasa ko mataimakin shugaban kasa. Sannan kuma tana da hurumin yanke hukunci akan wa'adin mulkin shugaban kasa ko mataimakinshi ya cika ko bai cika ba, ko kuma bada sanarwa cewa babu kowa akan kujerar.

**KOTUN KOLI**

Kotun koli itace mafi girman kotu a tsarin kotunan Najeriya, kuma itace kotu ta karshe wajen daukaka kara daga kotunan dake kasanta. Sannan kuma tana da hurumi na musamman akan hukunci tsakanin gwamnatocin jiha da gwamnatin tarayya da kuma rikicin tsakanin jihohi. Hukuncin kotun koli akan duk wata harkalla shine hukunci na karshe, ba za'a iya daukaka kara gaba ba. Hukuncin kotun koli doka ne a sauran kotuna.

**KOTUN DA BA TA GWAMNATI BA**

Su irin wadannan kotuna ana kirkirar sune a cikin al'umma. Ba gwamnati bace ke kirkirasu. Suna samun inganci daga amincewar al'ummar da ta kirkira su, wadda suke aiki a cikinta. So da dama shuwagabannin al'umma na gargajiya sune suke gudanar da wadannan kotuna. Gurfana gaban irin wadannan kotuna al'amarine na ra'ayi, kuma hukuncinsu ba tabbatacce bane. Tana yiwuwa hukuncin su ya zama mai karfi idan duk al'umma sun yarda da wannan hukuncin. Masu anguwanni da Dagatai da sauran masu sarautar gargajiya sukan zartar da al'amari don inganta zamantakewa a tsakanin al'ummarsu. Abu ne mai muhimmaci a tuntubi irin wadannan kotuna a cikin wasu al'amura, musamman ma a yankunan karkara.

**KAI KARA GA HUKUMA**

Ya kamata mu lura cewa kai kara ga hukuma a cikin harkallar dake gaban dan-agajin adalci na nuna cewa al'amari ya kai makura. A ko da yaushe ka fara sanar da duk bangarorin da harkallar tashafa akan zabin da suke dashi, da kuma irin sakamakon da bin kowane zabi zai haifar. A misali, kana iya bada shawarar kai ziyara, ko aikawa da wasikar neman hakki zuwa ga wata hukuma. Kuma zaka iya mika al'amari zuwa ga wata ma'aikata ko kungiya wadda kasan zata iya taimaka ma mutanen da kake huldar dasu. A misali kana iya mika al'amarin zuwa ga hukumar kare hakkin dan-adam. Wurin da kaga cewa kai kara shine mafi dacewar mataki, abin shawara a nan shine, ka tutunbi FIDA ko NBA, ko wani kwararen lauya da aka hada ka dashi, don tattaunawa da samun shawara akan hanya mafi kyau wurin tafiyar da wannan sha'ani. Idan kuwa an aikata wani laifi ne ko kuma ana azabtarwa ne, to kayi hanzari ka sanar a ofishin 'yan sanda. 'Yan sanda

zasu rubuta rahoton da ka kawo san nan kuma su fara bincike akai. (A lura cewa, gabatar da mai laifi gaban kuliya, nauyine da ya rataya a wuyan ‘yan sanda ko ofishin kwamishinan shari’a. Sabo da shi aikata laifi sabama dokar kasa ne ba wai shi wanda aka cutar kakai ne aka sabawa ba, don haka ana gabatar da mai laifi gaban kuliya don a gamsar da jama’a duk da yake dai akwai wanda mai laifin ya cutar daban).

Da zarar ‘yan sanda ko kwamishinan shari’a ya tabatar da cewa ana zargin mutum da aikata wani laifi to sai a shigar da ƙ ararshi gaban kotun da tayi dai-dai da sauraren irin wannan karar. A wani lokaci ma,sai a kamo shi mutumin da ake zargin. Kotun da za’a gabatar ma karar ta daganta da yanayi da kuma nauyin laifin da ake zargin mutum da aikatawa. Sai dai mafi yawan harkalloli sukan kai gaban kotun yanki, ko ta majistire ko kuma babbar kotu.

Amma a wannan laifaffukan, idan duk bangarorin musulmai ne, kuma sun amince ayi masu hukunci da dokar musulunci, to akan yi shari’ar a kotun shari’ar musulunci. Wata hanyar yin shari’a a kan laifuffukan itace yin shari’a kotun majistire to anan fa duk sunan da aka ba karar dashi za’a yi aiki. Kuma shari’ar a rubuce ake yinta.

**SHIRIN GURFANA GABAN KOTUN SHARI’AR MUSULUNCI KO TA AL’ADA**

Kotunan shari’a da na al’ada kotunan ne na ga-da-ga, don haka, ba dole bane lauya ya shiga. To amma fa idan ka kawo lauyanka, kotun zata yi na’am da aikin shi. Zaka iya zuwa kotun ka yanko sammaci ga mutum min da ya keta hakkin wanda yazo maka da harkallarshi. Maga-takardar kotun musulunci zai bada sammacin tuhuma akan aikata laifi ko akan neman hakki, dai-dai da karar da akayi. Daga nan kotun zata bukaci mutumin ya halarci kotun sannan sai a fara shari’a. kamar kowace harkallar laifi, za’a karanto harkallar ka sannan a saurari uzurinka, san nan a gabatar da shaidu idan akwai bukatar hakan. A lura cewa, a kotunan musulunci,ana amfani da yaren mutanen dake wannan gari ne wurin yin shari’a.

# BABI NA 4

**DOKAR IYALI**

**GABATARWA**

Kamar yadda yake a mafi yawan wurare a duniya, haka ma a arewacin Najeriya mata sukan nemi shawarwari game da dokar iyali, ma'ana, game da zaman aure, saki, rikon da da gado. A matsayin dan-agajin adalci, wajibine ka ilmantu da wannan doka da kuma wadannan abubuwa da aka jero don aikin ka yayi tasari.

**AURE**

Ana iya daukar aure a matsayin wata tarayyar jinsi wadda doka ta amince dashi. A Najeriya, aure kashi biyu ne aka aminta dasu, sune:- auren mace daya namiji daya da kuma auren mata da yawa ga namiji daya. A Najeriya, hanyoyi uku ne mutane ke amfani dasu wurin kulla yarjejeniyar aure:

- Auren kotu
- Auren al'ada da kuma
- Auren musulunci.

Zamu duba al'amarin cancantar kulla yarjejeniya aure da kuma ingancin wannan yarjejeniya a tsarin duk wadan nan hanyoyi na kulla aure da muka fada.

**AUREN KOTU**

Auren kotu shine duk auren da aka kulla a karkashin dokar aure ta shekarar 1990

**INGANTACCEN AUREN KOTU SHINE WANDA YA CIKA WADANNAN SHARUDDAN**

- Dolene ya zamo duk bangarorin sun amince da kansu, kuma akan ganin damar su da wannan tarayya.

- Dole ne duk bangarorin su zamo basu da aure a dai-dai lokacin kulla wannan auren. Ma'ana ba zai inganta a kulla wannan aure ba a yayin da wani daga cikin bangarorin yana da wani auren.

- Dole ne kowane daga cikin bangarorin ya zama ya kai ko ya wuce shekara 21 da haihuwa. A yayin da daya daga cikin bangagorin ya gaza ma shekara 21 to dole ne ya kawo iyayen shi ko marikinshi ya shige gaba.

## KAFIN A SAMU INGANTACCEN AUREN KOTU, DOLE NE ABI WADANNAN MATAKAI

- Daya daga cikin bangarorin zai yi rubutattar rantsuwar kotu cewa ko da daya ne daga cikin iyayen bangarorin ya zamo mazaunin wannan jiha na akalla kwana 15 kafin ranar auren, kuma sun cika duk sauran sharuddan dake akwai na kotu.

- Doka ta wajabta ma daya daga cikin bangarorin ya sa hannu akan takardar niyyar aure wadda maga-takardar sashen adana bayanan aure na gwamnati zai basu, bayan an sa hannu sai a mayar da takardar inda aka karbota. Idan har bayan kwanaki 21 zuwa watanni ukku, babu wanda ya kalubalanci wannan niyya tasu ta aure, sai maga-takarda ya basu takardar shaidar aure. Amma idan aka samu kalubale, to mai kalubantar auren zai shigar da ja a wurin maga-takarda, daga nan sai a gabatar da al'amarin gaban alkali, a inda zai saurari hujjojin mai jayayya sannan ya yanke hukunci akan halacci ko haramcin auren a idon doka. Ana iya takaita wannan al'amari ta hanyar yanke wannan hukunci a dakin shawarar alkali ba tare da an zauna mashi a kotu ba.

## AKAN KALUBALANCI NIYYAR AURE DA WADANSU DALILAI KAMAR HAKA

- Idan daya daga cikin bangarorin yana da aure, don haka ya gaza cika sharadin auren kotu.

- Idan daya ko duka banagarorin suna da karanci shekaru, kuma basu sami amincewar iyaye ba wurin kulla auren.

- Idan daya daga cikin bangarorin ba shi da cikakken hankali da zai iya yin yarjejeniyar aure da karan kanshi.

- Ko kuma duk wani dalili mai kwari da ke iya sawa a hana bulla auren.

## YIN BIKIN AURE

Bayan an samu takardar shaidar kulla auren su ma'auratan na iya yin hidimar biki ta daya daga cikin wadannan hanyoyi.

## DAKIN KOTUN AURE

1. Ana iya yin bikin auren a cikin dakin daurin auren kotu daga karfe goma na safe (10 a.m) zuwa karfe hudu na yamma (4 p.m). Dole ne a bude kofofin dakin a yayin da ake bikin. Wajibi ne a samu shaidu akalla mutum biyu a wurin.

2. Ana iya yin shagalin bikin a wani wurin ibada a inda za'a samu wani sanannen Limami ko Fasto ya jagoranci bikin. Ana yin bikin tsakanin karfe takwas na safe (8 a.m) zuwa karfe shida na yamma (6 p.m), kuma a samu shaidu akalla mutum

biyu. Nan ma dole ne kofofin wurin ibadar su zama a bude. (Idan wurin ibadar bashi da takardar lasisin yin bikin aure to ba za'a kira wannan aure ingantaccen auren kotu ba.

3. Ana iya yin bikin a duk wurin da aka so yin shi idan an samo lasisi na musamman akan yin hakan.

**RUSHEWAR AUREN KOTU**

**HARAMTACCEN AURE**

A karkashin dokar aure, aure yana haramta (ma'ana aure yana rasa amincewar doka a matsayin halattacen auren kotu) a yayin da:

- Ya kasance daya daga cikin ma'aurata, a yayin kulla wannan auren, yana da wani auren da wani mutum daban.

- Duka bangarorin suke da wata dangataka ta jinni ko kusanci wadda ta haramta aure tsakanin su, wato idan su muharraman juna ne.

- Suka saba ma dokar aure a tsarin wuri da jama'ar da suke cikinta, inda suke kulla alakar auren nasu.

- A yayin da kaya ko duka daga cikin bangarorin bai amince da wannan alakar auren ba ko kuma ya amince ne a akan tilas ko akan yaudare.

- A yayin da aka samu kuskure a wurin shaidawa da sanayya game da daya daga cikin bangarorin , ko kuma kuskure a cikin yanayin bikin da ake yi ko kuma a yayin da daya daga cikin bangarorin ba zai iya fahimtar ma'anonin da ke cikin yarjejeniyar ba.

- A yayin da daya, ko duka bangarorin bai kai shekarun aure ba.

- Idan daya ko duka bangarorin bashi da cikakken hankalin da zai iya amincewa da yarjejeniyar aure don kanshi ba.

**AUREN DA ZA'A IYA HARAMTAWA**

Aure na zama wanda za'a iya haramtawa (wato wani daga cikin ma'auratan na iya neman a raba auren sabo da haramcin shi) idan ya kasance lokacin auren, daya daga cikin ma'auratan:

1. Ya gaza tabbatar da auren ta hanyar saduwa.

2. Bashi da cikakken hankali, ko yana da hauka, ko yana samun tabuwa lokaci-zuwa-lokaci, ko yana da farfadiya.

3. Yana fama da wata cuta da ake iya dauka wurin jima'i.

4. Idan matar tana dauke da cikin wani mutum daban da mijinta.

## SAKI A CIKIN AUREN KOTU

Kafin wani bangare, ko duka banagarorin ma'aurata su nemi a raba aure, dole ne ya zama sun kai a kalla shekara biyu da yin auren, kuma dole ne su bayyana cewa auren ya kai iyakar lalacewar da ba za'a iya gyara shi ba. Doka tana gamsuwa da rashin gyaruwar aure idan daya daga cikin wadannan yanayi suka tabbata.

a. Wanda ake karar ya cigaba da kekashewa wurin kin amincewa da jima'i da gangan.

b. Idan wanda ake karar ya yi zina a cikin auren shi kuma mai karar ya gaza jure ma ci gaba da zaman aure a wannan hali.

c. Wanda ake karar yana yin wata dabi'a mara kyau, wadda mai karar ba zai iya jurewa zama da shi ba da wannan dabi'ar.

d. Idan wanda ake karar ya ci gaba da kaurace ma mai karar har na fiye da tsawon shekara daya izuwa lokacin da aka shigar da karar.

e. Idan ma'auratan suka guje ma juna, kowa ne na zaune wuri daban har na tsawon shekara biyu.

f. Idan ma'auratan suka guje ma juna, kowa yana zaune wuri daban har na tsawon shekar biyu, kuma basu yi jayayya akan karar da aka shigar ba.

g. Idan wanda ake karar ya gaza yin biyayya ga dokar biyan hakkin aure.

h. Idan wanda ake karar bai halarci karar ba har tsawon lokacin da ake kyautata zaton ya mutu.

Wurin fara shari'ar neman saki, akwai bukatar shi wanda kake huldar da shi ya samu lauya d zai tsaya mashi wurin shigar da karar.  Idan alkali ya tabbatar da hujjojin da aka kafa wurin neman sakin to sai ya bada wa'adin biko (Decree Nisi) na tsawon wata uku. Ana iya yin haka ne da fatan cewa ma'auratan zasu sasanta kansu cikin wannan lokacin, amma idan hakan bata samu ba, har wa'adin biko ya wuce, to sai alkali ya raba auren (Decree Absolute).  A lokacin shigar da karar, Lauya na iya hadawa da kara akan ikon rikon 'ya'ya da rabon dukiya, da ciyarwa, da kudin da za'a rika biya daga lokaci-zuwa-lokaci na tsawon wani lokaci.

## AUREN AL'ADA

Auren al'ada halattaccen aure ne a tsarin dokar Najeriya. Tsarin auren yana bambanta daga wuri-zuwa-wuri, to amma akwai wadansu abubuwan da basu sauyawa kuma dole ne su tabbata kafin auren ya inganta.

## IKON KULLA YARJEJENIYAR AURE INGANTACCE

### SHEKARUN HAIHUWA

- A tsarin gargajiya, ba'a tsayar da takamaiman shekarun haihuwa, wanda sai an cika su kafin a kulla aure ba. Mafi yawa, akan yi amfani da balagar mutum ne wurin tabbatar da ya isa aure. Sai dai kuma wannan tsari yana fuskantar suka don ya saba ma 'yancin dan-adam, Sashe na 21 na dokar 'yancin 'ya'ya na cewa ba'a amince ma duk mutumin daya gaza shekara 18 yayi aure ba, idan hakan ta faru, to wannan auren ya haramta kuma ba'a amince da shi ba ala kulli-halin.

### AMINCEWA

- Amincewar mutum da aure a tsarin auren al'ada tana da bangare biyu: Amincewar masu auren da kuma amincewar iyaye. Dole ne a samu amincewar ma'auratan kafin a daura auren. Amincewar iyaye ma wajibi ne, kuma dole sai an samu kafin bikin auren ya inganta.

- A tsarin doka ba'a amince ma wanda keda wani auren ya sake yin wani auren ba.

- Dole ne auren ya zama a bisa ganin damar ma'auratan, kuma ya zamo da kudirin anyi shi ne rai-da-rai.

- Dole ne a tabbatar cewa ma'auratan ba 'yan-uwan juna na jinni bane sannan kuma sai an samu amincewar iyaye ko mariki kafin auren ya inganta.

- Doka bat a amince ma iyaye da su tilasta 'ya'yansu akan aure ba.

### BIYAN DUKIYAR AURE

Biyan dukiyar aure wani mahadi ne wanda ya wajaba a cikin auren al'ada kafin auren ya inganta. A Najeriya akan kira dukiyar aure da suna sadaki.

### BIKIN AURE

Abin da ake yi wurin biki ya bambanta daga wata al'umma zuwa wata, ana yin biki ne a lokacin da aka raka amarya zuwa gidan angonta. A wasu al'ummomin kuma ana yin bikin a lokacin da dangin ango suka biya sadaki ga dangin amarya. Ba kamar auren kotu ba, a auren al'ada namiji na auren fiye da mace daya a lokaci daya.

### RUSHEWAR AURE A TSARIN AUREN AL'ADA

Auren al'ada na rushewa a mafi yawan al'umma a yayin da mace ta bar gidan aurenta. A kan bukaci danginta da su biya wani kaso daga cikin kudin sadakin da mijin ya biya a wurin daurin aure. A wasu al'umomin akan bukaci mai bukatar raba aure ya kai kara don a warware auren a hukumance.

**AURE A KARKASHIN SHARI'AR MUSULUNCI**

Auren shari'ar musulunci yana da abubuwa da dama da suka zo dai-dai da na al'ada. Misali, ana bukatar namiji ya biya sadaki ko Mahar ga matar da yake niyyar aure. Sai dai kuma, a karkashin shari'ar musulunci, matar da za'a aura itace ake ba sadaki (mahar) ba iyayenta ba.

**ABUBUWAN DA KE TABBATAR DA INGANTACCEN AURE A SHARI'AR MUSULUNCI SUNE;**

**a. BADAWA DA KARBA**

Anan mahaifi, ko wakilinshi na angon zai roki mahaifi ko wakilinshi na amaryar daya bada auren 'yarshi (amarya) ga danshi (ango). Idan aka amsa rokon, sai Liman ko wani Malamin addini yayi addu'ar daurin aure a gaban jama'a wadanda sune shaidu.

**b. SAMUWAR BANGARORI DA KUMA AMINCEWARSU**

A wannan tsarin dokar ma'aurata na iya amince ma juna da aure ba tare da shamaki ba. Sai dai kuma, a mazhabar maliki, wadda itace ke aiki a Najeriya, uba na da 'yancin yanke shawarar aure a madadin dan karamin danshi da kuma 'yarshi budurwa (ijbar). Duk da yake dai wasu mazhabobin baya ga malikiyya sun amincewa uba ya bayar da 'ya'yanshi mata wadanda ke cikin budurcinsu ga aure, ba lalle sai sun amince da kansu ba, wannan ba shi bane ra'ayin mafi yawa daga mazhabobin sunni. Mafi yawan suna kan ra'ayin cewa dokar musulunci bata yarje ma iyaye su tilasta ma 'ya'ya akan aure ba. Misalin da za'a iya kafa hujja dashi akan wannan Magana shine, lokacin da Aliyu bn Abi-Talib ya nemi auren diyar Annabi Muhammad (S.A.W) wato Fatima, Annabi yace mashi ya jira sai ya nemi amincewarta domin kuwa ta ki amincewa da wasu maneman a baya. Bugu da kari kuma, wata buduwar ta kai kara ga Annabi (S.A.W) cewa mahaifinta ya bayar da auranta ba tare daya shaware ta ba. Sai Annabi (S.A.W) ya bata shawara cewa tabi umurnin mahaifinta. To amma data dara da cewa ita ba zata iya zaman aure da wanda bata so ba, sai yace mata ba lallai bane sai ta yi wannan auren. Tana iya zuwa ta auri wanda take kauna. Sabo da haka anan ya tabbata 'yancin uba ya yanke hukunci akan auren 'yarshi ba tabbatacce bane.

**c. SADAKI:** wannan shine dukiyar da ake bayarwa ga amarya ko iyayenta tsarin shari'ar musulunci ya yanke karancin sadaki, amma bai takai taba yawancin shi ba**.**

d. Waliyi ko al'wali na mata dana miji

e. Shaidu

f. Dokar musulunci ta haramta aure tsakanin wasu mutane sabo da dangataka ta jini, dangantakar auratayya, da sauransu.

g. **DAURIN AURE:** Auren musulunci ana daura shine a masllaci, ko agida ko a gaban wani malamin addinin musulunci tare da halartar shaidu musulmai akalla mutum biyu.

Kamar yadda yake a tsarin auren al'ada, haka ma a tsarin auren musulunci, mutum na iya auren fiye da mace daya. To amma, dole ne mutum ya tabbatar da adalci a tsakanin matan nashi.

"Ku auri matan da suka kwanta maku a rai, biyu ko uku, ko hudu, amma idan kuka ji tsoron rashin aikata adalci a tsakaninsu to ku tsaya ga daya.
(kur'an 4:3)

**CUTA DA KE TA HAKKI ACIKIN AURE**

Alkur'ani mai girma yayi gargadi mai tsanani akan mutum ya tabbatar da adalci a tsakanin matanshi, kuma ya tanadar masu duk bukatarsu na rayuwa.

"….. Kuma ku zauna dasu (matanku) cikin girmamawa ga juna. Idan ma kunji kuna kinsu a zuciyar ku ko kuna kin wani abu game da su, kuma da sannu Allah zai sanya alkhairi mai yawa acikin shi." (kur'an 4:19)

**KULLE:**

Wata dabi'a da tayi karfi a arewacin Najeriya itace ta tsare matan aure a gidajen su. Ana kiran wannan abu Furdah, kuma wasu masana fikihun addini suna ganin cewa wannan abu bashi da asali a musulunci. A ra'ayin wadannan masana, yin haka na hana wa mata shiga cikin hidimomin mutane da na siyasa, kuma yana hana su samun damar habaka tattalin arzikin su, ta hanyar shiga huddodin cinikayya da mutane. Duk da yake shari'ar musulunci bata yarda da cudanyar maza da mata ba tsari ba, bata kuma hana mata shiga su dama cikin huddodin zamantakewa da mutane da kuma huddodi cinikayya ba. Sai dai alkur'ani ya umarci mata da su zama masu kamun kai a cikin jama'a kuma su kyautata suturar su a mutunce. A takaice kada su karya dokar Allah.

"….. Kada ku zamo masu hila acikin Maganarku (da mutane) don kada wani mai raunin zuciya ya kamu da sha'awa; ku zamo masu tausasa murya a cikin maganarku. Kuma ku tausasa sauti acikin gidajenku, kuma kada ku rikayin ado irin na jan hankali (a waje) kamar irin na jahilan farko…" (kur'an 33:32)

"….. Ya kai annabi ka gaya ma matanka, da 'ya'yanka mata, da kuma muminai mata su lullube jikinsu a yayin da suke waje. Wannan shi ne mafi dacewa da yanayin da ya kamata a gansu a ciki. Allah mai yawan gafara ne mai jinkai" (kur'an 33:59).

Sannan kuma, Annabi (S.A.W) yace ma Saudat: Ku mata kuna iya fita daga gidajenku ma damar kuna da kwakkwaran dalilin yin hakan. daya daga cikin manyan dalilan dake fitar da mata daga gidajensu shine neman abinci, kuma

shari'ar musulunci ta amince wa mata yin hakan idan mazansu suka gaza ciyar dasu, da tufatar dasu da basu muhalli.

Abu Hanifa yace mace na iya yin alkalanci, wanda kuwa aikine dake bukatar mace ta fita daga gida taje wurin shari'a. Sannan kuma Umar ya nada wata mata ta kula da kasuwa, nan ma aikine wajen gida.

**RUSHEWAR AURE A SHARI'AR MUSULUNCI**

Duk da dai musulunci baya son saki, an bada damar yin hakan idan al'amari ya tsananta. A irin wadannan wurare, ana iya raba aure ko kuma ayi saki.

**HARAMTACCEN AURE A SHARI'AR MUSULUNCI**

A mazhabar malikiyya aure ya haramta tsakanin 'yan uwa na jini, makusanta, misali, uba daya, ko kuma idan aka yi auren bada nufin dorewa ba, na tsawon wani lokaci wato (auren mutu'ah) ko bada aron mata wato (muwakkat)

A tashin farko dai, yana da muhimmaci a lura cewa namiji ba zai iya furta saki uku a lokaci daya ba.  Alkur'ani mai girma ya fada a sura ta 2:129:

"Saki yana yiwuwa sau biyu ne ka dai…" Bayan saki na daya da na biyu, ma'aurata na iya sasanta junansu ba tare da bukatar sake daura aure ba. Amma idan akayi saki na uku, to aure tsakanin ma'auratan ya haramta har sai ita matar ta auri wani mutum daban ya sadu da ita ya sake ta sannan zasu iya sake aure.

Sannan kuma ana iya yin furucin saki gaban shaidu mutum biyu.  Sauran hanyoyin saki sune:

- **TALAK BA'IN BANUNA SUGRA:**  Wannan shine yayin da mijin ya bikaci mayar da auren baya cika iddar wata uku. A irin wannan yanayi dole ne sai an sake daura aure.

- **SAKI NA BIDI'A:**  wannan shine furucin sakin da bai cika sharuddan saki ba. Misali ga saki uku lokaci daya.

- **WAKILTA A GURIN SAKI:**  wannan shine idan aka wakilci miji wurin sakin matarshi, wato aka sakar mashi ita.

**AUREN  DA ZA'A IYA HARAMTAWA A SHARI'AR MUSULUNCI**

a. Idan ba'a samu amincewar iyaye ba, za'a iya raba aure.

b. Rashin biyan sadaki na iya sa a raba aure

c. Auren karamar yarinya; ko da an samu amincewar iyaye, idan aka aurar da karamar yarinya zata iya neman a warware auren yayin da ta girma kuma bata gamsu da auren ba.

## AURE MARAS TSARI (FASID)

A mazhabar malikiyya, musulmi ba zai iya aure fiye da mace hudu ba a lokaci daya. Idan ya auri ta biyar a yayin da yake da mata hudu, to bai kyautu ba kuma ya haramta. Aure mara tsari haramun ne. A na iya gyara shi ta hanyar mutum ya saki mata ta biyar din.

## SAKI A TSARIN SHARI'AR MUSULUNCI

Musulunci ya yarda da saki, kuma yana faruwa ta hanyoyi da dama daidai da yanayin da ya kawo saki.

## SAKI (DALAK)

Shi wannan saki shine furucin rabuwar aure daga miji. Shi ne mafi yawan hanyar rabuwar aure a arewacin Najeriya. Shi saki (Dalak) ana yin shi ne ta hanyar miji ya furta saki har sau uku kamar yadda Alkur'ani ya bayyana wurin tabbatar da rabuwar aure.

## AKWAI WASU LOKUTTA WADANDA BAI KYAUTU MIJI YA FURTA SAKI BA

1. Idan matar tana haila

2. Idan matar ba tayi tsarki ba kamar yadda Alkur'ani mai girma ya bayyana.

A lokacin da aka furta saki, kada namiji ya kori matar daga gidan shi har sai ta cika iddar kwana 90, idan kuma tana da ciki, to sai tayi kwana 90 bayan haihuwa.

## KHUL'U

Wannan shine rabuwar aure daga bukatar mace akan rabuwar shi. Alkur'ani ya amincewa mace ta kashe aurenta idan tana da dalilin kashe auren. Idan haka ta faru, to matar zata maida wa mijin kudin sadakin daya bata.

"….babu laifi akan kowanensu idan ta bayar da wani abu don a sahale mata." (Kur'an 2:229).

To amma a irin wannan sahalewa, Alkur'ani bai wajabta ma miji ya ci gaba da ciyar da matar ba.

## NEMAN SAKI A KOTU

Baya ga Khul'u, mace na iya shigar da kara ta nemi mijinta ya sake ta a kotun shari'ar musulunci. To amma dole ne ta tabbatar da kaya daga cikin wadannan abubuwa:

- Cewa mijinta ya na muzguna mata a bayyane ko ta hanyar cusa mata bakin ciki.
- Cewa mijinta ba shi da lafiyar mazakunta.
- Cewa mijinta ya gudu ya barta.
- Cewa mijinta yana dauke da wata cuta mai iya yaduwa zuwa ga wani, kuma wadda bata da alamun warkewa.
- Cewa mijinta ya gaza rike tada bukatunta na yau da kullun.
- **LI'AN:** Idan namiji ya zargi matar da zina amma kuma ba shi da shaida sai shi kanshi, ko kuma yayi ikirarin cewa wani ne yayi mata ciki ba shi ba.
- **ILA:** Idan namijin yayi alkawarin kauracewa matar shi da kwanciyar aure na tsawon lokacin da ya zarta wata hudu kamar yadda Alkur'ani ya tanada.
- **ZIHAR:** Idan mutum ya kwatanta matarshi da mahaifiyarshi, to dole ne sai yayi kaffara ko dai ya ciyar da mabukata mutum sittin ko ya yi azumin wata biyu a jere. Idan ba haka ba matar na iya neman ya sake ta.

Idan saki ya zama irin na kotu, to kotun na iya yanke hukuncin cewa mijin ya ci gaba da ciyar da matar bayan auren ya rabu har tsawon wani lokaci.

**MUBARAH:** Wannan kuma na faruwa ne a lokacin da duka ma'aurata suka amince da su raba aurensu.

**CIYARWA**

**NAFAKA:** A tsarin dokar musulunci, wajibine mijin ya ci gaba da ciyar da matarshi a yayin da yake aurenta da kuma lokacin da suka rabu, sai dai idan matar tayi hul'u ne. Nauyin da ke kanshi ya hada da abinci, muhalli, tufafi da duk abubuwan da take bukata na wajibin rayuwa, madamar yana da ikon samar da shi. Don haka musulunci yayi hani ga mutum da kada yayi aure idan yasan bashi da ikon rike matar.

"su wadanda suka rasa halin yin aure to su kame kansu (daga fasikanci) har sai Allah ya hore masu daga taskarshi (kur'an 24:33)

Kuma alkur'ani mai girma ya fada cewa:

“Ku ciyar da matanku da irin abin da kuke ci, ka da ku wulakanta su, kuma kada ku musguna masu…

Mutumin da yake da hali to ya ciyar gwargwadon halinshi…” Kuran 2:233).

Bugu da kari, musulunci ya hukunta a cikin Alkur’ani cewa dukiyar da mace ta mallaka kafin aure da kuma cikin aure hakkinta ne, kuma tana da ikon amfani da ita yadda ta so.

Mijinta ba zai iya shiga cikin harkokin dukiyarta ba sai in taba shi izinin shiga.

**HAKKI BAYAN SAKI**

Matan da suka yi auren kotu basu da hakki kai tsaye daga mazan su, sai dai idan suka shigar da kara akan abasu abinda ake kira alimony, wato kudaden da zasu ci gaba da tafiyar da rayuwarsu dasu bayan saki har zuwa wani lokaci kayyadajje, to alkali na iya bada umarni a kasa dukiyar da ma’aurata suka tara a lokacin aurensu, aba matar wani kaso.

Auren al’ada shima baya da wani hakki bayan saki. Mace na iya kwashe duk kayan da ta shigo dasu gidan mijinta , to amma bata da hakkin wani abu da zai bata bayan saki. Sai dai kuma tana iya samun kudin rikon da.

Dokar musulunci ta bukaci miji daya ci gaba daba matar ciyarwa har wani lokaci bayan saki. Alkur’ani yana kokarin kare mata kada a wahalar dasu ba bisa ka’ida ba, ta hanyar cewa ba za’a kore su daga gidajen mazansu ba har sai sun kamala iddah, kuma mazansu su ci gaba da ciayar dasu suna basu abubawan bukatar rayuwa har sai wa’adin ya cika.

“…(maza) su cigaba da daukar nauyin ciyarwa da tufatarwa akan adalci.” (kur’an 2:223).

Kuma shari’ar musulunci ta bukaci mutum ya bayar da wata kyauta ta ganin dama yayin rabuwar aure.

“… kuma kayi masu baiwa ta kyautatawa, mai dukiya ya bayar dai-dai karfinshi, matalauci ma ya bayar dai-dai karfinshi. Baiwa mai tsoka tana ga wanda ya kyautata”. (kur’an 2:236)

An amince ma mace tayi karar mijinta akan ya bata hakkokinta na bayan saki a tsarin shari’ar musulunci. Kotun da tafi dacewa a kaima irin wannan kara itace kotun shari’ar musulunci. To amma zai fi kyau a fara kokarin sasanci a tsakanin mijin da matar shi.

**‘YA’YA DA RIKONSU**

**MATSAYIN AL’AMARIN A TSARIN AUREN KOTU:-** Mutanen da sukayi irin wannan aure, to alkali zai yi shari’ar wanda keda ikon rike ‘ya’ya tsakanin mijin da matar idan wannan yana cikin abubuwan da aka shigar da kara a kai. Abinda alkali yake dubawa wurin yanke shari’ar wanda zai rike ‘ya’yan da aka samu a cikin auren shine:- menene zai fi alfanu ga yaran da ake shari’ar a kansu. Idan aka ba uwa rikon ‘ya’yan, to za’a bukaci miji ya rika bada hakin ciyarwa ga uwar don ta iya tafiyar da rayuwarsu. Tana yiwuwa kuma kotu ta bada umarnin ayi tarayya wurin rikon ‘ya’yan. Anan ‘ya’yan zasu zanna tare da baban su, na wani lokaci. Misali, ‘ya’ya suna iya zama wurin mahaifiyarsu tsawon lokaci da ake karatu a makaranta, sannan su koma wurin babansu suyi hutu a lokacin da aka bada hutu a makaranta, ko kuma karshen mako, abu mafi kyau shine iyaye su zauna su yi shawarar abin da zai fi alfanu garesu da kuma ‘ya’yansu, maimakon su bar kotu ta yanke masu hukunci akan hakan. Gaskiyar lamari shine, ita kanta kotu tafi son ayi hakan.

**A TSARIN DOKAR AL’ADA:-** Al’amarin yana bambanta daga al’ada zuwa al’ada. Amma a mafi yawan al’adu idan aka samu jayayya akan rikon ‘ya’ya, to ‘ya’yan sukan zauna wurin babansu. To amma fa uwar tana da cikakkar damar tuntubar ‘ya’yanta a duk lokacin da taso. Idan yaran kanana ne, to ana barwa uwar ta rike su don ta kula dasu suna kanana. Bayan sun zama matasa to sai su koma wurin babansu.

**A TSARIN SHARI’AR MUSULUNCI:-** Nauyin ciyar da ‘ya’ya da mata duka yana kan namiji. Idan ya gaza yin hakan uwar ‘ya’yan na iya yin karar shi a kotu. Idan saki ya faru ko suka rabu, shari’ar musulunci ta bukaci uwa ta rike ‘ya’yanta har sai sun balaga idan maza ne, idan mata ne kuma har sai sun yi aure.

Alkur’ani yayi umarni a ba mace mai shayarwa ladar shayarwa dan da aka haifa a cikin aure.

…..Kuma idan su (mata da aka saki) suna shayarwa, to ku basu ladar shayarwa. Sai ku yi shawara dasu akan abinda ya dace kuma ya kyautatu da a biya su. Idan al’amari ya tsananta, to sai a ba wata matar daban ta shayar da dan ga namiji.” (Kuran 65:6).

“Iyaye mata zasu shayar da ‘ya’yansu na tsawon shekara biyu cikakku, ga wanda ya so ya cika adadi. To shi (namiji) zai biya ladar shayarwa akan adalci. Babu wani rai da za’a dora ma nauyin daba zai iya dauka ba. Babu wata uwa da za’a yi wa abin da bai kyautu ba sabo da danta, haka kuma babu wani uba da za’a yi ma haka sabo da danshi. Haka duk wani magaji ma za’a yi mashi. Idan kuma suka yi yarjejeniya akan yaye, bayan sun tuntubi juna, to babu laifi akansu, idan kuma

kaso bayar dadanka raino to babu laifi a kanka, ma-damar ka biya mai raino ladarta da adalci. Amma kuji tsoron Allah, kuma ku sani cewa Allah na gani kuma ya san abin da kuke aikatawa."
(Kuran 2:223).

Shi uba, ana sa ran ya biya ladar rikon 'ya'yanshi (wanda ya hade da abinci, wurin zama, kiwon lafiya da karatu) ga 'ya'ya mata, har sai sun yi aure, ga 'ya'ya maza, har sai sun isa neman na kansu. Amma idan

sun zamo suna da karfin rike kansu, to babu tilas akan babansu ya rike su.

# BABI NA 5

## GADO

Al'amarin gado yana da matukar rikici da rudani musamman ga matan da mijinsu ya mutu ya barsu wadanda nauyin rainon 'ya'yansu yakan dawo kansu, bayan rasuwar mazansu. Gado yana komawa karkashin dokar iyali, kuma yana danganta da idan mamacin ya rubuta wasiyya, da kuma irin auren da suka yi, da kuma dokar al'ada da suke bi. A nan kasa, zamu yi bayanin sha'anin gadon mace dai-dai da wadannan ma'aunai da muka fada.

a. **GADON MACE A TSARIN AUREN KOTU:** A karkashinn irin wannan aure duka mata da mijinta zasu iya gadon junansu, kuma dukkansu suna da hakki dai-dai da juna a cikin gadon dukiya, ko da kuwa babu wasiyya, kuma ko wacce irin al'ada suka bi. Abin dubawa a nan shine, tunda har mijin ya amince yayi auren kotu, to ya zabi ayi amfani da tsarin dokar auren kotu wurin hukunci akan lamarinshi. To amma, ya fi kyau a rubuta wasiyya don a tabbatar da amfani da manufofin mamacin a matsayin abu mafi muhimmaci. Yin hakan zai rage bata lokaci da rudani wanda ke tattare da al'amarin rabon gado, wanda kuma yake sawa a taushe wa mata hakki.

   **Rashin Wasiyya:** Sha'anin rabon gadon mutumin da ya mutu bai bar wasiyya ba yana da matukar rikici, kuma yana bambanta daga jiha zuwa jiha.

b. **GADON MACE A TSARIN AUREN AL'ADA:** Kamar yadda aka bayyana a baya, dokokin al'ada suna bambanta daga wuri zuwa wuri, kuma suna bin zamani. Duk da haka abinda aka fi amfani dashi a mafi yawan al'adu shine, mace bata gadon kayan mijinta bayan ya mutu. To amma idan ya rubuta wasiyya wadda a cikinta ya bayyana cewa ya bayar da wata dukiya ga matarshi, to za'a iyar da nufinshi. Don haka yana da muhimmaci ku ba mutanen da kuke hulda da su shawara akan rubuta wasiyya.

c. **GADO A KARKASHIN SHARI'AR MUSULUNCI:** A tsarin shari'a ta musulunci, matar mamacin daya mutu ba tare da rubuta wasiyya ba tana da gadon kashi daya bisa hudu na dukiyar shi bayan an biya basussuka. Idan kuma yana da 'ya'ya da jikoki, to kasonta zai dawo daya bisa takwas. Idan suna da yawa (matan aure) to su duka zasu raba kashi daya bisa hudu ko daya bisa takwas. To amma idan mace ta mutu, to mijinta zai gaji kashi daya bisa biyu (wato rabi) na dukiyar da ta bari, bayan an biya basussuka.

Idan mace ta fita daga musulunci to ba za ta yi gado ba. Dokar musulunci bata amince ma mutum ya rabar da dukiyarshi duka da kanshi kafin mutuwarshi ba. To amma an amince ma mutum yayi wasiyya da kashi daya bisa uku na dukiya amma wasiyyar ana yinta ne ga mutumin da bashi cikin magada. Abin lura anan shine, idan mutum ya so yin wasiyya to ba lallai bane ya raba wasiyyar kamar yadda ake rabon gado a tsarin musulunci, yana iya raba wasiyyarshi yadda ya so.

## RABON GADO A MUSULUNCI

a) Uba – daya bisa shida (1/6)

b) Kaka Namiji – daya bisa shida (1/6)

c) Uwa – daya bisa shida (1/6) idan tana da da ko daya bisa uku 1/3 idan bata da da

d) Kaka mace - daya bisa shida (1/6) idan tana da da ko daya bisa uku (1/3) idan bata da.

e) Miji - daya bisa hudu (1/4) idan da da ko daya bisa biyu (1/2) idan babu da.

f) Matar ko matan aure -daya bisa takwas (1/8) idan da da ko daya bisa hudu (1/4) idan babu da.

g) ‘Ya – rabi (1/2) idan ita kadai ce ko biyu bisa uku idan da ‘ya’ya maza da yawa.

h) ‘Yar da (jika) zai samu kamar na sama.

i) Dan-uwa na ciki daya (shakiki) daya bisa shida (1/6) idan shi kadai ne ko daya bisa uku idan suna da yawa.

j) ‘Yar-uwa ta wajen uwa-daya bisa shida (1/6)idan ita kadaice ko biyu bisa uku (2/3) idan suna da yawa.

k) ‘Yar-uwa shakikiya - Rabi (1/2) idan ita kadaice biyu bisa uku (2/3) idan suna da yawa.

“Maza suna da nasu kaso, mata ma suna da nasu kaso daga abinda iyaye suka bari da kuma abinda ma kusanta suka bari, ko da dukiyar na da yawa ko ‘yar kadan ce, kaso na shari’a.”(kur’an 4:7)

## BAIWA (KYAUTA)

Kamar yadda muka gani a baya, wasiyya na kiyaye wa mace hakkin ta na gado. Don haka yana da kyau ku fadakar da mutanen da kuke hulda dasu akan su yi kokari mazansu na aure su rubuta wasiyya. Ko kuma miji na iya yima matarshi

kyautar dukiya kafin rasuwarshi a shari'ance, ta hanyar baiwa, musamman ma idan dukiyar ta shafi kasa (fili, gida ko gona da sauransu). Idan irin wannan kyauta ta faru a cikin lokacin aure to yana da kyau matar ta tabbatar da an rubuta takardar yarjejeniyar kyauta daga mijin ta zuwa gare ta. Sannan kuma a tabbatar da cewa wannan takardar shaidar kyauta an kaita kotu an buga mata hatimi. Kuma a samu shaidu a kalla mutum biyu su sa hannun sun shaida da wannan kyauta ta dukiya da mijin ya baiwa matarshi. Da zaran akayi haka, to dukiyar ta tashi daga mallakar mijin ta koma mallakar mata, don haka ba za'a iya lissafata cikin dukiyar gado ba. Tabbatar da rubutawa da sa hannu zai ba matar natsuwa. Ko ba komai dai, tana da hujjar da zata nuna ta tabbatar da ba'a lissafa wannan dukiya cikin dukiyar gado ba.

## WASIYYA

Wasiyya tana fara tasiri ne a lokacin da marubucin ta ya rasu. Amma ana iya janye ta a yayin da yake raye. Ana iya janye ta gaba daya ko kuma ayi mata yan canje-canje. Sai dai kuma ana so a duk lokacin da mutum zai rubuta wasiyya to ya kudurta a ransashi cewa itace wasiyyar shi ta karshe. Idan mai rubuta wasiyyar yana da tabin hankali, to ba za`a samu wannan kuduri daga gareshi ba, haka kuma idan an tilasta mutum ya rubuta wasiyyar ne.

**IKON RUBUTA WASIYYA:-** kowane mutum na da ikon rubuta wasiyya, ko da kuwa mutumin nan na karkashin dokar al`ada.

## MUTANEN DA BA YARDA DA WASIYYAR SU BA.

a) Karamin yaro

b) Mai tabin hankali

c) Makaho wanda bai iya karatu da rubutu ba dole ne a kula don guje ma zamba wurin gudanar da wasiyyar

d) Idan aka tabbatar akwai zamba ko tilasci wurin rubuta wasiyyar

## SHARUDDAN RUBUTA WASIYYA A HUKUMANCE

a) Dole ta zamo a rubuce

b) Dole a sa mata hannu

c) Dole a samu shaidu biyu ko fiye, wadanda aka rubuta ta aka sa mata hannu a gabansu.

d) Shaidu zasu rubuta furucin shaida, kuma su sa hannu akan amincewar su da yin shaidar a gaban mai wasiyyar.

## INGANCIN WASIYYA

a) Dole ne mai wasiyya yayi kudurin cewa itace wasiyyar shi ta karshe

b) Dole ne mai wasiyya ya zama ba karamin yaro bane

c) Dole ne mai wasiyya ya zamo yana da cikakken hankali

d) Dole ne wasiyya ta zamo rubutatta, kuma asa mata hannu kuma shaidu su shaida

e) Dole ne a rubuta kwanan wata kuma asa hannu a kowane shafi na wasiyyar

**ABUBUWAN DA KE CIKIN WASIYYA**

a) Sunan ka da adireshinka da mahaifarka

b) Sunaye da kwatancen wadanda zasu ci gajiyar wasiyyar

c) Bayyanannen rabon dukiyar da aka bari

d) Bayanannen suna da kwatancen wanda zai zartar da wasiyyar

e) Hannayen jari na kamfanoni

f) Masu bi da wadanda ake bin bashi

g) Akawun na banki

h) Bayanin sigar dukiya

i) Duk wani bayanin da ka san yana da alaka

**AJIYAR WASIYYA**

Ana iya ajiye wasiyya a babbar kotu, ko wurin jami'in kulawa ko banki, ko wani kamfanin lauyoyi ko wani amintaccen aboki.

**SAMUN TAKARDAR GUDANARWA**

Idan mutum ya mutu bai bar wasiyya ba, to matarshi, ko mijinta idan macece, ko wani dan uwa na jini wanda keda ra'ayin iyar da nufin mamacin na iya neman takardar izinin gudanar wa daga kotu.

Dole ne sai matar ko mijin ya kawo ma kotu takardar shaidar mutuwa, da takardar shaidar aure, da duk wata takarda dake da alaka wadda zata tabbatar da gaskiyar Magana, sannan kuma  a rubuta takardar neman a hukumance don neman takardar izinin gudanar da rabon gadon mamacin.

Daga nan sai kotu tayi sanarwa ga jama'a tare da neman idan akwai wani mai ja akan wannan kuduri to yazo yaja. Idan ba'a samu wata jayayya daga wani mutum ko wasu mutane ba, kuma kotu ta gamsu da mutumin da ya nemi izini akan cewa zai iya isar da nufin mamacin, to sai ta bayar da takardar izini gareshi.

# BABI NA 6

## HAKKIN MATA, DA HAKKIN DAN-ADAM

Hakkin dan-adam na nufin jimillar hakkokin da kowane dan-adam ya cancanci ya samu, ba tare da la'akari da kabila, kasa, al'ada, jinsi shekaru, addini ko wani matsayi ba. Kowane dan-adam ya cancanci ya samu kowane daya daga wadannan hakkoki dai-dai da kowa, ba tare da wariya ba.

A matsayin 'yan-agajin adalci yana da muhimmanci ku zama kun ilmantu da hakkokin dan- adam da kuma yadda za'a zartar dasu a Najeriya. Yana da kyau kusan abin da kundin tsarin mulkin Najeriya ya tanada da kuma yadda tanadin ke tasiri ga rayuwar mata da sauran mutane dai-daiku.  Ku sani cewa mata ba zasu kawo maku matsalar keta hakkin su ka dai ba, a'a zasu iya kawo maku matsalar keta hakkin mazan su dana 'ya'yansu.

A zamanin mulkin soja a Najeriya, ana kama mutane, a tsare su a gallaza masu harma a kashe su ba tare da wani laifi ba. Wadannan  sune mafiya yawan hanyoyin keta hakkin dan-adam da suka zama ruwan dare a wancan lokacin, kuma wadannan hakkokine da mutane da dama yanzu sun san su.

Sai dai kuma, kundin tsarin mulkin Najeriya na (1999) yayi tanaje-tanaje da suka wuce maganar hani akan gallazawa, wato 'yancin rayuwa da kuma 'yancin sauraro da adalci. Don haka yana da kyau kayi kyakkyawan nazarin kiyayewar da kundin tsarin mulki ya tanada ga dan-adam.

A tarihi, yancin dan-adam ya samo asali ne tun daga lokacin da mutune suka fara tunanin abinda ya kyautu, wanda idan akayi shi anyi adalci ga al'ummansu. Guggubin zalinci na bayan yakin duniya na II shine ya jawo shuwagabanni suka zauna suka tattauna abinda yafi kyautuwa ga al'umominsu. Sun bi diddiki wurin samo asalin hakkin dan-adam daga akidojin addinai da al'adu. Sabo da haka ne a shekarar (1984) duniya tayi ittifaki akan hakkokin dan-adam na matakin farko na duniya baki daya. Za'a iya samun wadannan hakkoki rubuce a cikin kundin hakkin dan-adam na duniya (UDHR). Duk kan hakkokin da ke cikin kundin yarjejeniyar  kasa da kasa na duniya da kuma wakanda ke cikin kundin tsarin mulkin Najeriya sun samu ingancin sune daga UDHR. Shi UDHR, shine ya ja ragamar kirkiro wasu dokokin yancin dan-adam, wadanda suka alkiblanci fannonin hakkin zaman takewa, da hakkin siyasa, da hakki akan bunkasa tattalin arziki,da hakkin al'adu da gargajiya, da kuma hakkin mata da kuma hakkin su na a daina yi masu ko wacce irin wariya, da hakkin na kasassu, da sauran su.

## YANCIN DAN ADAM NA MATAKIN FARKO, BABI NA 4 DAGA KUNDIN TSARIN MULKIN NAJERIYA.

Ga takaitaccen bayani akan yancin dan adam na matakin farko, kamar yadda kundin tsarin mulkin najeriya ya tana da. Akwai cikakkun bayyanan wadan nan bangarori na tsarin mulki a kunshe cikin jerin littatafan da keda nasaba da wan nan littafi.

1. ‘**YANCIN RAYUWA:- (**Sashe na 33). Wannan yankin ya tanaji Kariya ga rayuwar dan kasa, kuma cewa babu wanda ke da hurumin daukar rai na wani mutum face idan kotu ce ta yanke mashi hukuncin kisa daidai da wani laifi da yayi, wanda kuma kotun ta tabbatar da laifin.

Sai dai kuma ba za’a dauka mutum yayi kisan kai ba idan:

- Ya/ta yi hakan ne ta hanyar kare kanta/shi ko dukiyar ta/shi
- Ya/ta yi hakan ne a kokarin kiyaye tsare wani wanda ake tsare akan doka wanda ke kokarin tsarewa, ko kuma wurin kama wani mai laifi
- Ya/ta yi hakan ne a kokarin murkushe zanga-zanga, ko murkushe yinkurin wasu mutane don juya gwamnati, ko murkushe ‘yan tawaye ga doka

2. **YANCIN MUTUNCIN MUTANE (SASHE NA 34):-** Wannan ‘yanci yayi tanadi akan cewa:-

‘Yan kasa na da ‘yancin a dubi al’amarin su cikin girma da arziki a matsayin suna ‘yan-adam.

Babu wani dan kasa da za’a bautar ko a tilasta shi zama karkashi hukuncin wani mutum ko a gallaza mashi ko a kaskantar dashi, ko a tilasta shi yayi wani aiki.

Wannan dokar tayi hani akan kaskantar da mace kamar binne ta da rai saboda ta aikata wani laifi, ko kuntata mata a zuci ko a aikace, saboda ta rasa mijinta, ko ayi mata aure ba bisa son ranta ba, ko tilasta ta yin wani abu mai cutarwa na al’ada kamar yadda yake faruwa a wasu al’umma. A wasu al’umma akanyi wa mata fyade ko a kashe su, bisa kazafin maita.

3. **HAKKI AKAN YANCIN BIN AKIDA, IMANI DA KUMA ADDINI (SASHE NA 38):**

- Ko wanne mutum na da yancin bin duk addinin da yaso, ko kungiyar addinin da yaso .
- Ko wanne mutum na da yancin sauya addininshi
- Ko wanne mutum nada yancin yada addininshi, ko yada manufar abinda yayi imani da shi ta hanyar koyarwa, ko aikatawa ko dabi’antuwa da tafarkin addini.
- Babu wani mutum da zai je wani wurin neman ilimi da za’a tilasta mashi aikata wani abu na ibada wanda ya saba ma addinin iyayenshi.

- Babu wata al'ummar addini da za'a hana ta koyar da yaransu darussan addini a duk wani wurin koyarwa da al'ummar ke girmamawa.

- An haramta ma mutane kirkirawa da shiga kungiyoyin asiri.

**4. 'YANCIN BAYYANA RA'AYI DA AIKIN JARIDA (SASHE NA 39):** Wannan hakki ya tanadi cewa:

- 'Yancin mutum akan bayyana ra'ayinshi a fili ba tare da takura ba.

- 'Yancin mutum akan ya rike ra'ayinshi kuma ya yada manufar wannan ra'ayi. Dole ne irin wannan ra'ayi ya zamo na hakika idan ba haka ba kuwa za'a iya tuhumar mutum akan yada batanci game da wanda aka yi ra'ayi akanshi.

- 'Yancin mutum na ya mallaki gidan jarida ko gidan talabijin madamar shi mutumin ya samo izini daga hukumar da abin ya shafa.

**5. 'YANCIN GUDANAR DA ZANGA-ZANGAR LUMANA DA HADA GWIWA (SASHE NA 40) :** Wannan 'yancin ya tanadi cewa:

Kowane mutum nada 'yancin gudanar da zanga-zangar lumana da kuma hada gwigwa da wanda yaso.

Kowane mutum na da 'yancin shiga kowace jam'iyyar siyasa, ko kungiya sana'a ko kuma kowacce irin kungiyar hadin gwiwa daya so'

Dole ne jam'iyyun siyasa su zamo a kan tsarin Hukumar Zabe ta kasa (INEC).

**6. 'YANCIN SAURARO DA ADALCI (SASHE NA 36):** Wanna 'yanci ya tanadi cewa:

- Dole ne kotu ta saurari kowanne mutum ba tare da bambaci ba kuma ta zama bata dogara da ra'ayin kowa ba wurin yanke hukunci.

- Dole kotu tayi shari'a a bainar jama'a, sai dai idan wanda za'a yi ma shari'ar dan kasa da shekara 18 ne ko kuma ana so a kare tashin-taashina a cikin al'umma.

- Duk wanda ake tuhuma, to bashi da laifi har sai idan wata kotu ta tabbatar da laifin nashi.

- Ba za'a hana wani wanda ake tuhuma damar tuntubar lauyan shi ba.

- Babu mutumin da za'a gurfaanar a tuhume shi gaban kotu sau biyu akan laifi daya.

**7. HAKKI AKAN 'YANCIN WALWALA (SASHE NA 35):** Wannan hakki ya tanadi cewa:

Babu mutumin da za'a hana ma walwala face idan daya daga cikin wadannan abubuwan ne suka faru:

- Idan aka tuhumi mutum kuma aka tabbatar da laifinshi a wata kotu ingantatta.'
- Idan ana kokarin gurfanar da mutumin da yaki amasa kiran shari'a.
- Idan ana kokarin tilastawa mutumin da bai kai shekara 18 ba game da karatunshi ko wani abu na ci gaban rayuwarshi.
- Ana iya tsare mutumin da ke dauke da wata cuta mai yaduwa ta iska don ayi mashi magani, ko dan tsaron lafiyar jama'a.
- Idan aka kori mutum daga kasa ko kuma idan za'a mayar da mutum wata kasar da yayi laifi ya gudo daga can.

1. **'YANCIN SIRRI A CIKIN AL'AMARIN MUTUM DA KUMA CIKIN AL'AMARIN IYALINSHI (SASHE NA 37):** Wanna 'yanci ya kunshi:
    - Kare sirrorin kowane dan kasa da kuma sirrin gidanshi, da huddodin shi da jama'a, da firarshi a wayar tarho, da sakwaninshi na na'urar tangaraho.
2. **HAKKI AKAN 'YANCIN ZIRGA-ZIRGA (SASHI NA 41):-** Wannan hakki ya tanadi cewa kowanne dan dasa na da 'yancin yin zirga-zirga a sake a duk fadin Najeriya kuma yana iya zama a kowane bangare na kasar. Babu wani dan kasa da za'a kora daga Najeriya, ko a hana mashi shiga ko fita daga kasar face akan daya cikin wadannan dalilai:
    - Dan a hana mutumin da kotu ta tabbatar da laifinshi daga tserewa daga Najeriya
    - Don kokarin mayar da mutumin da aka kama da laifi zuwa kasar da yayi laifi
    - Idan aka kama mutum da laifi a kotu kuma aka yanke mashi hukuncin tsarewa a gidan yari a wata kasa wajen Najeriya.
3. **HAKKI AKAN YANCIN WARIYA (SASHE NA 42):-** Wannan hakki ya tanadi cewa:-
    - Babu wani mutum dan wata al'umma, ko mabiyin wani addini ko wata kabila, ko dan asalin wani wuri, ko dan wani jinsi ko mabiyin wani ra'ayi na siyasa da za'a yima wariya a gwamnatance ko game da daukar wani mataki a dalilin jinsin shi, ko addinin shi ko siyasar shi ko asalin shi da sauran su.

- Babu wani dan kasa da za'a nuna ma wariya ko a nakasa shi ko a murkushe shi a dalilin yana yin haihuwar shi (ma'ana wanda aka Haifa bata hanyar aure ba).

4. **YANCIN SAMU DA KUMA MALLAKAR KADARA (SASHE NA 43):-**

   Wannan 'yanci ya bada damar kowanne dan kasa na iya mallakar kadara a ko ina a fddin asar nan.

5. **HARAMCI AKAN TILASTAWA WURIN KARBAR KADARA (SASHE NA 44):**

   Wannan doka ta amince ma gwamnatin tarayya ko ta jiha ta karbi kadarar wani mutum ko wasu mutane, to amma sai an bi matakan da doka ta tanada, kuma dole a biya mutum diyya nan take idan aka karbar mashi kadarar shi.

**WASU HAKKOKIN NA DAN ADAM**

**B. HAKKIN MUTUM AKAN KASA DA HAKKIN HABAKA TATTALIN ARZIKI**

An bayyana hakkokin mutun akan kasar shi a matsayin duk wata gajiya da kowane dan kasa zai iya samu sabo da amincewar da yayi kasa ta mulke shi akan wasu tsarin dokoki ta hanyar jami'ai na kasa da na siyasa. Ana kiran wadannan hakkoki da hakkokin da suka jibanci tsaro, saboda suna bada tsaro akan tattalin arziki da na kasancewa dan kasa, kuma ana kiran su da hakkoki na karni na biyu. Sun hada da:

- Hakkin ilmantarwa
- Hakkin aikin yi
- Hakkin kiwon lafiya
- Hakkin muhalli
- Hakkin biya dai-dai a aiyukan da suke dai-dai da juna
- Hakki akan ingantaccen yanayin rayuwa
- Hakki akan samar da abinci
- Hakki akan zamantakewa
- Karancin albashin dan dasa mai kima

- Hakki  akan kula da tsaffi da kuma fansho.

Acikin kundin tsari mulki na 1999, an yi bayanin wadannan hakkoi a matsayin "Buri da manufofin dokar kasa" Ba za'a iya yin hukunci dasu ba a kotunan Najeriya.

## HAKKOKIN MATA HAKKOKIN DAN-ADAM NE

## AL'AMARIN HAKKIN MATA

Daya daga  cikin mafiya muhimanci a cikin manufofin 'yancin dan-adam shine daidaito a tsakanin mutane.  Da Musulmi da Kiristanci duk sun yi nuni da cewa kowanne mutum dai-dai yake da kowa a gaban Ubangiji, kuma miji da mata mataimakan juna ne Kur'an 2:223).  Haka nan kuma duk addinan sunyi Allah wadai da safarar mutane da duk wata hanya da ake amfani da ita wurin zalunci a wurin saduwa. Kuma duk sun amince ma mace ta mallaki dukiya.

Gwamnati itace ke dauke da nauyin kiyaye hakkokin 'yan kasa ta hanyar duk bangarorin ta.  Kowane dan kasa na da wadansnan hakkoki, ba tare da la'akari da jinsin shi ba. Don haka mata suna da kwatankwacin hakki akan kiyaye hakkokinsu kamar yadda kowane dan kasa yake dashi. Duk da haka kuma akwai wasu hakkoki na dan-adam wadanda akeyi don mata kadai. Saboda amincewa da haka ne Najeriya ta rattafa hannu akan yunkuri kasa da kasa don kawar da duk wani nau'in wariya ga mata (CEDAW), wadda itace dokar ta duniya mafi kammaluwa game da hakkokin mata. Akwai kwafen wannan doka a cikin jerin litattafan  da keda nasaba da wannan littafi a karshen littafin, don ku samu damar sabawa  da ita, kuma kusan hurumin wannan yarjejeniya ta kasa da kasa wajen kare hakkokin mata.

Uku daga cikin sanannun abubuwan keta hakkin mata sune auren dole, zalunci a gida da kuma hana su ilimi.

## AUREN DOLE

**DOKA BATA YARDA DA AUREN DOLE BA TA KOWANE HALI.** Haka kuma, babu wani tsarin aure da ake yi a Najeriya da ya yarda dashi. Sannan kuma, yin hakan zai zama hujja wajen rushe wannan aure. Auren dole keta hakkin mace ne na: darattawa, walwalar mutum, da kuma 'yancin bin ra'ayi da bin abinda mutum yayi imani akan shi. Ta wani bangaren, za'a iya kwatanta shi da wani salon bautarwa a zamanance, don haka haramtaccen abune.

Wata rana wata budurwa tazo wurin annabin rahama (SAW) tace baban ta ya aurar da ita ga wani mutum ba bisa san ran taba. Sai annabi ya bata damar ta ki auren.

Duk matar da ta samu kanta a cikin halin auren dole ga mijin da bata so to wajibine ta dauki mataki na gangawa. Sannan kuma zata samu kariya idan taje kotu. An saba kashe aure a kotun daukaka kara ta shari'ar musulunci idan aka samu cewa anyi auren bada amincewar matar ba.

## ZALUNCI A GIDA

Al'amarin zalunci a gida wani abune da aka saba gani a Najeriya. Yana iya zama zalunci na fili ko kuma na cusa kunci a zuciya, ko wani mataki daya zarta kima wanda wani ke amfani da shi wurin bada umarni da hukunci ga dayan a rayuwar cikin gida. Irin wannan kan faru tsakanin wasu makusanta juna, ko ma'aurata, iyaye da yayansu, ko mai aikin gida da mai gida, uwargida. A mafi yawan lokutta, yakan hada da cutarwa ta zahiri (duka, ingiza, bankadewa da sauransu) da kuma cutarwa ta hanyar saduwa (saduwa da karfi ko ta hanyar da ba'aso).

Irin wannan zalunci na iya zamowa na kullum, tana yiwuwa kuma ya faru sau daya.

Matsalar irin wannan keta hakkin dan-adam din shine, har yanzu ba'a dauki zalunci a gida a matsayin laifi a idon doka ba. Yan sanda da sauran jami'an tsaro na kallon al'amarin a matsayin wani abu na hidimar mutum ta ciki, wadda bai kamata suyi katsa landan ba.

Kashi tamanin da takwas bisa dari na harkallolin zalunci a gida suna faruwa ne ga mata. Kuma an bayyana shi a matsayin daya daga sanadin mutuwa da nakasa ta dun-dun-dun ga mata. Don haka yana da kyau ga 'yan-agajin adalci su dauki wannan al'amari da matukar muhimmanci. Idan mata, ko yara mata suka kawo rahoton zaluncin a gida. Sun kawo kuka ne na neman agajin gaugawa, don haka dole ne mu taimaka masu ta hanyar da ta dace. Idan muka duba batun hakki, to an keta hakkin suna darattawa, kuma yana iya kaiwa ga keta hakkin su na rayuwa.

Zamu tatauna cutarwa game da saduwa da cikakken bayani a babi na baga. Zamu fi mayar da hankali akan nau'o'in cutarwa ta zahiri a cikin wannan babin.

**AZABTARWA TA ZAHIRI A CIKIN GIDA**

Wajen duba al'amarin azabtawa ta zahiri a cikin gida ya kamata mu fadakar da kawunan mu game da wasu maganganu da wasu mutane ke tallatawa a tsakanin jama'a. Misali, wasu sukan ce ai duk wanda kaga an azabtar irin haka agida to ba makawa irin matan nan ne masu "taurin kai" ko irin "wawayen"masu aiki wadanda idan ba an azabtar dasu ba ba zasu taba fahimtar abinda ake nuna masu ba. Wata maganar da ake amfani da ita kuma itace: ai wannan wani abu ne wanda yayi dai dai a cikin rayuwar gidaje, ana yin hakanne don gyara tarbiyya. Ko dayake dai sanannen abune cewa za'a iya amfani da wani dan horo ga yara a wasu wurare, ba zai taba karbuwa ga tsarin dokar Najeriya ba, ayi amfani da gallazawa ta zahiri ga babbar mace, don haka dole ne a fadakar game da haka.

**YAYA ZAKU YI KU TAIMAKI WADDA TA KUBUCE DAGA AZABTARWA A GIDA?**

- Zaku iya shirya wata tattaunawar jan hankali tsakanin mai cutarwar da matar da ake cutarwar donganin ya daina amfani da hanyar cutarwar akanta.

- Zaku iya tattara wani taron sasanci wanda ya kunshi dangi ko abokai don sasanci tsakanin ma'auratan kuma a bukace shi da barin wannan zalunci. 'Yan uwan matar nada matukar muhimmanci anan, don su zasu bata mafaka har sai an tabbatar an warware matsalar
- Zaku iya kaiwa ga mai anguwa ko hakimi don ya sasanci, kuma ya ja kunnen mai cutarwar.

- Zaku iya gayyato wani malamin addini wanda ake darattawa ya sasanci

- Zaku iyakai kara ga ‘yan sanda
- Zaku iya neman agajin FIDA

Tunkarar ‘yan sanda da rahoton zalunci cikin gida wata badakala ce wadda da yawa daga cikin ‘yan-agajin adalci suke fuskata. To amma ya kamata ku gane cewa yin hakan na iya zama ceton rai da kuma hani a kan ci gaba da cutarwa.

**ILIMIN YAYA MATA**

Tsarin mulki Najeriya ya haramta kowace irin wariya, ta kowace hanya da ko wane irin salo kuma ya bayyana cewa kowane dan kasa yana da hakkin ilmantarwa. A gabaci da yammacin Najeriya akwai karacin irin wariyar da ke hana ma ‘ya’ya mata karatu. Amma a arewa ana yawan dakushe ‘ya’ya mata wajen zuwa makaranta. To amma alkur’ani yayi hani da irin wannan. Kuma yayi umarni cewa iyaye suke dauke da nauyin ilmintarwa a tarbiyyantar da ‘ya’yan su, kuma ya bayyana cewa da ‘ya’ya maza da ‘ya’ya mata duk suna da hakki a ilmantar dasu. Shari’ar musulunci tayi umurni ga dukkan musulmi, ba tare da la’akari da jinsin su ba akan su nemi ilimi. Sanannen abune cewa a tarihin musulunci, Annabi (SAW) ya rika ba mata darasi a lokacin da suka bukaci ya rika basu darasi suma, a wani kebantaccen lokaci.

**HAKKIN ‘YA’YA**

‘Ya’ya suna da wata daraja ta musamman a cikin al’umma. San nan kuma sun kasance sune mafiya rauni a cikin jama’a, su da mata, musamman ‘ya’ya mata. ‘Ya’ya mata suna fuskantar hadurra acikin gida da kuma wajen gida: sune suka fi yawa a cikin masu tallace tallace akan tituna kuma sune mafiya yawa daga cikin ‘ya’yan da basu zuwa makaranta.

Akwai rubuce-rubuce da dokoki da tsarin manufofi da dama da akayi don inganta jin dadi da walwalar yara a duk fadin duniya. Daga cikin su akwai yunkurin majalisar dinkin Duniya akan hakkin da (1989), wanda fiye da kasashe 190 suka rattafa hannu akan shi, cikinsu hadda Najeriya. Idan muka dawo yankin Afurka kuwa, akwai wadannan hakkoki a cikin kundin Afurka na Hakkin jin dadi da walwalar da, wanda da yawa daga cikin kasashen dake karkashin kungiya hadin kan kasashen Afurka (AU) suka rattafa hannu akai.

Dokar Hakkin yara ta zama ‘yar gida a Najeriya a shekarar 2003. Wannan dokar ta taattara mafi yawa daga dokoki da manufofin yunkurin majalisar dinkin Duniya akan hakkin da, hadi da dokokin cikin gida na Najeriya, wadanda suka shafi yara. Dokar an tanade tane don ta “tanadar kuma ta kiyaye” hakkokin yara ‘yan Najeriya, da kuma abubuwan da suka shafi wannan.

**WANENE YARO NE?**

Yaro kamar yadda dokar hakkin yara ta 2003 ta bayyana, shine duk wanda bai kai shekar 18 ba.

**MENENE DA MENENE HAKKOKIN YARA?**

Ma'anar hakkin yara a takaice shine duk wani abu da ya wajaba a basu sabo da a inganta tarbiyyarsu ko don shari'a ta wajabta abasu.  Don haka ana iya cewa: hakkin yara shine duk abinda ya wajaba a basu don kawai suna yara.

Wadannan hakkoki sun hada da :

- Hani akan: auradda karamin yaro, baikon karamin yaro, yima yaro zane ko tsaga, ko saka yaro cikin halin sha, sarrafawa ko dillancin miyagun kwayoyi.

- Hani akan: Amfani da yara wurin aiyukan laifi, gudu daga gida ko dauke yaro hadi da sake mashi mariki ba bisa ka'ida ba, sa yaro aikin karfi na tilas ko mai hadari ko "kura da shan duka gardi da karbe kudi". Wanda ya hada da sa yaro aiki a matsayin dan aikin gida a wani gida da ba nasu ba.

- Hakki akan rada suna, zama dan kasa da dai-daito da saura da kariya daga cin zarafi ta hanyar saduwa.

- Kariya daga cin zarafi da rashin kula da kuma kariya daga aikin da zai cutar da lafiya ko rayuwar yaro.

- Kariya ga yaron da bashi da dangi da kare sirrin shi.

**CUTAR DA YARA MATA**

A takaice dai cutar da yaro na nufin musgunawa ta zahiri ko a dabi'ance ko  ta hanyar cusa bakin ciki a zuci. Yana da ma'anar wasu abubuwa da ake yi ma yaro akai-akai ko jefi-jefi, wanda iyaye ko masu bada kula ga yaro suke yi, wanda ke cutar da yaron.  Wasu nau'o'in cutarwa ga yara mata sun hada da rashin kula, cutarwa ta zahiri, cutarwa  a dabi'ance ko cusa bakin ciki a zuci ko cutarwa ta hanyar saduwa.

**SA YARA MATA AIKIN WAHALA**

Sa yara mata aikin wahala wata hanya ce da ta ci gaba da zama game-gari, da ake amfani da ita wurin cutar da yara.  Ya hada da sa yara aiki a cikin yanayin da zai cutar da lafiyarsu, na tsawon lokaci mai gajiyarwa kuma akan kudi kalilan.  Abin da ke kara lalata al'amarin shine mafi yawan  lokutta, shi yaron da ake cutarwa bai san hadarin da ke tattare da wannan aiki ba, kuma bashi da ilmin hanyar kare kai daga irin wannan hadari. daya daga cikin hanyoyin sa yaro aikin wahala a Najeriya shi ne yaron gida.  Da yawa daga cikin 'yan Najeriya, harda masu fadi aji, suna da hannu dumu-dumu a cikin irin wannan aika-aika.

**FATAUCIN YARA MATA:**  Wannan ma wata hanya ce ta sa yara aikin wahala a Najeriya.  Itace hanyar nemo yaran aiki, tare da kamala su daga wani gari zuwa wani, tare da ajiyesu ko karbar su don a sa su aikin wahala.  Haka na faruwa a cikin kasa daya ko kuma daga wata kasa zuwa wata.  Sakamakon karshe shine sai a sa yara mata karuwanci ko a sasu aikin gida.  Akan amfani da yara maza wurin wanke mota ko su zama yaran mota, da sauransu.

Wani abun kuma da, shima, yayi yawa a Najeriya shine sa yara barace-barace da tallace-tallace akan tituna. Sau da dama akan bayar da hayar yaro musamman a cikin dangi a rika amfani da shi wurin barace-barace. Za'a iya ganinsu a duk titunan Najeriya idan aka duba. Ana yin tallace-tallace ne ta hanyar sa yara su rika siyar da kaya haja akan tituna, mafi yawa don su taimaki iyayensu. Yaran da suka sami kansu a wannan hali suna fuskantar hadurra musamman yanayin yadda ababen hawa ke guje-guje akan tituna, sannan kuma za'a iya cutar dasu ta wasu hanyoyin ma.

Wata hanyar kuma da ake bi wurin keta hakkin dan-adam itace bada hayar yara mata don ayi zina da su. Anan ana amfani da yara mata su zama karuwai ko abin da ake kira masu kasuwancin zina. Yin haka na tura yara su dauki cututtukan da ake samu ta hanyar saduwa, ko su yi cikin banza ko su sami rauni a matancin su da sauran bala'o'i.

Dokar kare hakkin yara ta Najeriya ta shekarar 2003 tayi suka da Allah – wadai da kakkausan harshe akan duk wani nau'in aikin wahala da ake sa yara. Sashe na 21-40 na dokar ya tanadi'yancin yara ta hanyar hani akan sa yara aiki na dole, ko mai hadari ko "Kura da shan duka….." wanda ya hada da aiki a matsayin yaron gida a gidan da ba na su ba.

**CUTARWA TA HANYAR SADUWA:** Shine ida babban mutum ke amfani da karancin shekaru da rauni na yara mata ya yaudaresu suyi wasu abubuwa da suka shafi jima'i, ko ta hanyar karfi, wanda ake nuna fifikon shi akan yaran ko ta hanyar dabara, ta yadda yaran ba zasu iya fahimtar sakamakon abinda aka jefa su cikin aikatawa ba.

**NAU'O'IN CUTARWA TA HANYAR SADUWA:** Sun hada da yin lalata da yarinyar da keda dangantaka ta jini (misali tsakanin uba da 'ya), ko kuma fyade, wannan kuma shine yin amfani da karfi don yin lalata da wani ko da namiji ne ko mace. Fyade na da matukar rikitarwa musamman ga yara, don haka yana zuwa tare da karin cutarwa ta zahiri ko ta dabi'a. Yin jima'i da karamin yaro, ko da yaron ya amince laifi ne ana kallon shi a matsayin cutar da yaro ta hanyar saduwa sabo da yaron bashi da isasshen hankalin da zai iya yanke shawara mai ma'ana.

Karuwancin yara na cutarwa ne ga yaran ta hanyar saduwa. Ya kunshi sa yara yin lalata don a basu kudi ko wata alfarma.

**BARAZANAR SADUWA:** Ita kuma wata hanyar cutar wace dangane da saduwa wadda ake yinta ta hanyar yawan zolaya ko kunyatarwa ko yin maganar da bata dace ba game da wasu sassan jiki da yawan matsawa da maganganun batsa da sauransu.

A bangaren na III na dokar kare hakkin yara wato (CRA) an bada kariya ga yara da nuna wariya da abubuwan cutarwa. Takamaimai ma sashe na 21 ya haramta auradda kanannan yara kuma ya tanadi horo ga duk wanda ya karya dokar. Horon shine idan aka tabbatar da laifin mutum za'a yi mashi tara har naira dubu dari biyar, ko shekara biyar a gidan yari, ko duka biyun. Haka kuma sashe na 21-40 ya haramta sauran nau'o'in cutar da yara irin su baikon karamin yaro (ma'ana a sa ranar auren yaro da wani mutum), ko yin tsaga ko tilasta yaro ya gudu daga gida, ko sanya yaro aikin wahala (kamar yadda aka yi bayani a baya), ko barace-barace, ko karuwanci, ko lalata da yara da dai sauran hanyoyin lalata (kamar yadda aka jero su a baya).

Dokar CRA tayi nuni ga bukatar yaro ya taso cikin dangi don ya smu natsuwa akan asalin shi da kuma cewar yana da "Kowa". Don haka ta hana a raba yaro da dangin shi ba bisa

son ranshi ba sai dai idan anyi hakan ne don fa'idantuwar yaron. Bugu da kari, don a kiyaye yara daga cutarwa, sashe na 50-52 na dokar CRA sunyi tanadi akan kariya ga yara, dake bukatar kariya daga cutarwa ta zahiri ko ta tarbiyya. Ta bada hurumi ga jami'in kula da tarbiyar yara, ko dan sanda, ko kuma duk wani jami'i ya kawo duk yaron da aka samu yana cikin bukatar kulawa da kariya gaban kotu don daukar matakan gyara, idan an samu cikakkar hujjar da zata sa a yarda cewa yaron maraya ne, ko dangin shi sun gudu an bar shi, ko an watsar da shi ba kula ko iyayen shi ko marikanshi suna cutar da shi da gallaza mashi ko an saka shi cikin tasku ko ya samu tabin hankali ko yana ta bi layi ba shi da dangi ko kuma ya nakasa sosai, ko yana barace-barace, ko yana tare da wani sananne barawo ko karuwa ko kuma ya kangare ma iyaye ko ya shiga halin da keda hadari ga rayuwa da lafiya da tarbiyyar shi.

**ABINDA YA KAMATA 'YAN-AGAJIN ADALCI SUYI IDAN SUKA SAMU YARON DA KE BUKATAR TAIMAKON GARGAWA:**

- A tuntubi yaron don a gane matsalar shi
- A kai rahoto ofishin 'yan sanda ko gidan horon yara mafi kusa.
- A bibiyi tafiyar al'amarin don a tabbatar da an nemo iyayen yaron ko marikanshi ko kuma duk wanda ya cutar da shi.
- A nace wurin tabbatar an yi ma yaron adalci kamar yadda dokar kare hakkin dan-adam ta tanada.

**HANYOYIN DA AKE BI WURIN TABBATAR DA SAMUN HAKKI KAMAR YADDA KUNDIN TSARIN MULKI YA TANADA**

- Sashi na 46 na tsarin mulkin shekar 1999 yayi tanadi a kan cewa duk mutumin da yake ikirarin cewa an keta, ko ana kokarin keta hakkinshi sai ya kai kara ga Babbar Kotun Jiha ko Babbar Kotun Tarayya don a bashi damar kwatar hakkin shi.
- Kuma ana iya mika al'amarin ga jami'an karamr hukuma.
- Kuma ana iya mika al'amarin ga kungiyoyin kare hakkin dan-adam ta kasa (NHRC).

**A KARKASHIN DOKOKIN ADDINI KUMA:**

- A kai kara ga jagoran addini na garin game da wannan keta hakki.
- A kai kara ga 'yan Sanda.
- A kai kara kotun shari'ar musulunci.

- A kai al-amarin ga wasu hukumomi warware badakala ko wata hukumar gwamnati.

**ILIMI NA DA MATUKAR MUHIMMANCI**

An gano cewa mafi yawan matan dake zuwa gaban kotu basu da masaniyar hakkokin su, don haka sai su bada sararin da za’a iya kara keta hakkin su. Idan zaku je wurin wani masanin addini to ku tabbatar kun haddace duk ayoyin Al’kur’ani ko na Bible wadanda suke kafa hujja a kan abinda kuke ikirari. Sannan idan zaku je kotun shari’ar musulunci ko kotun zamani ku tabbatar kuna da sani akan hujjojin da zaka kafa, da karfin hujjojin, kuma ku tambayi masu baku shawara akan doka (lauyoyi).

# BABI NA 7

**DOKAR LAIFUFFUKA**

**LAIFUFFUKA AKAN MATA FANNIN SADUWA**

Hulda da shari'a wani sabon abu ne wurin mutane da yawa, don haka akwai wasu dabarun aiki da suka wajaba ku kware da su. Mata sukan zo da al'amuransu su sa nemi shawararku akan abubuwan da suka shafi shari'a a matsayin masu kai kara ko a matsayin wadanda akai kara. Don haka yana da kyau ku san hanyoyin da ake bi wurin cika takardar kara, ko samun beli, ko sammaci da sauransu.

- Laifuffuka akan mata fanning saduwa.
- Kashe-kashen laifuffukan saduwa da hukuncinsu a tsarin doka.
- Wadanda aka yi ma fyade ko aka ci zarafinsu ta hanyar saduwa.

**AN BAYYANA FYADE A CIKIN SASHE NA 282 NA DOKAR LAIFUFFUKA A MATSAYIN:**

"Duk mutumin da yayi jima'i da wata mata ta daya daga cikin wadannan hanyoyi to yayi fyade:

a) Ba bisa yardar taba

b) Ba tare da saninta ba

c) Koda da saninta ne idan akayi amfani da ban tsoro da barazanar kisa

d) Ko da saninta ne idan mutum ya san cewa shi ba mijinta bane, amma ita tana zaton cewa shi mijinta ne

e) Koda da amincewarta idan har bata kai shekara sha-hudu ba, ko kuma bata da cikakken hankali."

Dokar laifuffuka wadda ake hukunci da ita a arewacin Najeriya tana bayar da horon shekara 14 a gidan yari ga wanda aka kama da laifin fyade. Sai dai kuma a tsarin dokar laifuffuka ta shari'ar musulunci ta jihar Kano ana yanke hukuncin kisa ga wanda yayi

fyade idan ya taba aure. Idan mai fyaden bai taba aure ba, to ana yanke hukuncin bulala 100. Kuma za'a iya bashi daurin rai-da-rai.

Abin lura anan shine, ko da matar ba tayi kokarin hana mai yi mata fyade cin nasara ba, fyade ne dai idan har bata amince ta sadu da shi ba. A wasu lokuttan, mata sukan gaza kokari wurin dakushe yunkurin mai yi masu fyade sabo d tsoron raunatarwa ko kisa.

## YADDA AKE FUSKANTAR SHA'ANIN FYADE/KO WANDA AKA CI ZARAFINSHI/TA TA HANYAR SADUWA

- A tattara hujjoji bakin gwargado – Wannan kuwa ya hada da kin yin wanka ko wanke wata alama, da haka ne malaman asibiti zasu iya samun samfarin maniyyi don ya zama hujja, kuma likita zai iya duba duk wata kswarzana da kujewa don ya rubuta rahoto akai.

- Ayi gaugawar zuwa asibita don samu rahoton likita da kuma taimakon gaugawa don kariya daga cututtuka.

- A kai rahoto ga 'yan sanda da wuri bakin iyakar iko.

- A tabbatar wanda abun ya faru a kanshi ya samu tallafi kuma ba'a barshi shi kadai tare da dan sandan da bai damu da jinsi ba.

- 'Yan sanda zasu yi bincika daga nan su kuma kamo wanda yayi aika-aikar su gurfanar dashi gaban kuliya.

- Ba kasafai ake bayar da beli akan wannan laifi ba.

## TSANTSAR RASHIN KAMUN-KAI

Doka na kokarin kare yara daga cin zarafi irin na rashin kamun-kai don haka akayi tanadi na musamman na dokar da bata bukatar samun abubuwa da ke nuna saduwa kai tsaye wajen kama mutum da laifin fyade ba. Wannan doka tana kokarin kare yara daga rashin kama-kai na miyagun malaman makaranta, ko iyaye ko wasu mahukunta.

Sashe na 285 yayi tanadi kan duk wanda yayi wani abu dake nuna tsantsar rashin kamun kai ga wani mutum wanda jinsinsu ya bambanta ba tare da aamincewar shi ba ta hanyar amfani da karfi ko barazana ko ya tilastawa mutumin akan biye mashi cikin wannan dabi'a to za'a hora shi da tsaro a gidan yari wanda zai iya haura shekara bakwai kuma za'a iya yi mashi tara, kuma ko da yaro ya amince a cikin aikata wannan dabi'a tare da malamin shi, ko marikinshi ko duk wani mutumin da aka ba amanar shi in har yaron bai kai shekara 16 ba, ba za'a dauke ta a matsayin amincewa ba a tsarin wannan dokar.

## HAKKIN WANDA AKA CUTAR

Abu na farko kuma mafi muhimmaci daga hakkin wanda aka cutar ta hanyar saduwa shine a sama shi adalci, don haka, a matsayin ‘yan agajin-adalci dole ne kiyi rahoton DUK WATA harkallar da ta shafi cutarwa ta hanyar saduwa zuwa ga ‘yan sanda kuma a nace akan ganin an gurfanar dasu gaban kotun da ta dace.

Babban kuskuren da ake yi shine a dauka cewa yin hakan zai kunyatar da wadda aka cutar din kuma ya zubar da kimarta. To sai dai, dole ne akai al’amarin kotu don kare wasu a gaba kuma don tabbatar da adalci ga wanda aka cutar.

**TUHUMA AKAN ZINA**

Tsarin shari’ar musulunci, haramtaccen jima’i da jima’i kafin aure da lalata tsakanin manya duk laifi ne. Haramtaccen jima’i (zina) ana yanke mata hukuncin kisa ta hanyar jefewa idan mai laifin ya taba aure. Idan bai taba aure ba to hukuncin bulala dari ne. To sai dai kuma akwai dokoki masu tsauri wurin bada hujjar zina, kuma idan aka rasa wani abu cikin sharuddan kafa hujja, to ba za’a iya kama matar da laifin zina ba. Wurin tabbar da laifin zina akan mutum, dole ne, a samu shaidu mutum hudu adalai wadanda suka ga faruwar zinar (tirmi-da-tabarya) a lokaci daya, ko kuma mutum yayi ikirari da kanshi a gaban kotu cewa yayi zina, ko a samu mace da ciki ba ta hanyar aure ba. A lura cewa kungiyoyi kare hakkin dan-adam sun soki hukuncin zina akan mace yafi sauki akan kafa hujja akan namiji.

A lura cewa Kundin tsarin mulkin Najeriya yayi tanadi cewa duk matar da aka kama kuma aka tsare za’a sanar da ita (da yaren da take fahimta) dalilai da hujjojin da suka sa aka kama ta ko aka tsare ta cikin awa ashirin da hudu. Sannan kuma tana da halin biyan lauyan da zai kareta a gaban kotu.

# BABI NA 8

## DOKAR LAIFUFFUKA – KAMU DA BELI

## KAMU

Kama mutum ba tare da wata cikakkar hujja ba keta hakkin mutum ne. Doka ta nuna cewa kowa mai gaskiya ne har sai an tabbatar da laifin shi. Kundin tsarin Mulkin Najeriya, da kuma kundin Alkawarin Duniya akan Hakkokin Dan-Adam na Zama Dan kasa da na siyasa sun bayyana sharuddan kamu da tsarewa da kuma hakkokin mutum da suka danganci kamu da tsarewa. (a duba karin bayani akan wannan doka a cikin jerin littattafan da ke da nasaba da wannan littafin a karshen littafin).

## MA'ANAR KALMOMIN DA SUKA SHAFI TSAREWA

| | | |
|---|---|---|
| 1. | Kamu (arrest) | Kamu shine jami'an tsaro su nemo mutum su kawo shi gaban hukuma sabo da zargin ya aikata wani laifi. |
| 2. | Tsarre (detainee) | Tsararre shine duk mutumin da aka hana mashi walwala sabo da dalilan bincike ko don za'ayi mashi shari'a akan wani laifi ko fursunan yaki ne da sauransu banda mutumin da aka tabbatar da laifinshi, ana kiran wannan da fursuna. |
| 3. | Tsarewa (Detention) | Wannan ya hada hana mutum walwala sabo da dalilin binciken laifi, ko kafin shari'a ko wani dalili na daban. |
| 4. | Fursuna (Prisoner) | Fursuna shine duk mutumin da aka hana ma walwala saboda an tabbatar da laifinshi a kotu. |
| 5. | Yari (Prison) | Tsaro bayan an tabbatar da laifi. |

## KAMU DA TSAREWA

Idan aka kama mutum, to dole ne a sanar da shi/ita, nan take, dalilin kamu, kuma dole ne a bata/shi bayani a rubuce cikin awa ashirin da hudu. Ya/ta na da 'yancin kin fadar komai har sai ya/ta tattatauna da lauyanta/shi. Doka ta tanadi cewa kada 'yan sanda su tsare mutum fiye da awa arba'in da takwas (48) ba tare da an kaishi gaban kuliya ba sai idan kuwa laifin ya danganci wanda za'a yi ma hukunci kisa.

**BELI**

Beli shine saki daga tsaro na wani lokaci kafin a kamala bincike ko shari'a. A wannan yanayi wanda ake zargi da laifi da kuma wanda ya tsaya mashi zasu rubuta rubutaccen alkawari cewa zasu halarta a wani bayyannanen wuri da aka bukacesu da kuma bayyananen lokaci don amsa tuhuma akan laifin da ake zargin mutumin da aikatawa. Dalilin cewa doka taba kowa gaskiya har sai idan an tabbatar da laifinshi, shi yasa ake bada beli don gudun kada ayi ta tsare mutum bisa kuskure, har sai an gama bincike wurin

'yan sanda ko shari'a a kotu. Babu wani tsari na musamman da doka ta tanada game da yadda ake karbar beli. Ana iya bada beli ko da kamuwar kudi ko ba kamuwar kudi. Kamuwa wata kaddara ce ko kudin da ake karba a rike don a tabbatar cewa wanda aka yi belin nashi bai tsere ba. SHI BELI KYAUTA NE, KUMA DA MAZA DA MATA DUK SUNA IYA TSAYA WA MUTUM SUYI BELIN SHI. A wasu lokutta 'yan sanda na iya kin bada beli ko da kuwa ba laifin baya cikin jerin manya-manyan laifuffuka idan:

- Tsararen ba shi da wani sanannan wurin da za'a iya samun shi ko da yaushe aka so samunshi ko kuma idan akwai shakku akan wurin daya fada.
- Ida ana zargin cewa zai ketare beli ya tsere.
- Ida ana gudun cewa zai hana ruwa gudu wurin bincike.
- Ida ana zargin cewa zai je ya kara aikata wani laifin idan aka sake shi.

Da zarar aka gurfanar da wanda ake zargi da laifi gaban kotu to belin da 'yan sanda suka bada ya kare, sai kuma an rubuta takardar neman beli daga kotu. Ba kowane laifi ne ake iya yin beli akan shi ba, daga wurin 'yan sanda kafin shar'ia. Misali, kisan kai ko kuma duk laifin dake dauke da hukuncin kisa ba'a bada belin sa. Ga irin wadannan laifuka, alkali ne kadai ke iya bada beli idan aka kawo al'amarin kotu. Kotu kuma na iya ganin damar badawa ko hana beli.

Abubuwan da kotu kan duba wurin yanke shawarar hana beli sune:

- Idan akwai yiwuwar mutumin zai ketare beli ya gudu, ko
- Idan akwai yiwuwa mutum zai yi ma kotu katsalandan wurin gudanar da bincike, ko
- Idan mutumin ya saba aikata laifi ko,
- Idan tsare mutumin yafi allheri don kiyaye shi daga hadari.

**KETARE BELI**

Idan wanda akayi beli ya tsere ko ya "ketare beli", alkali ko majistire zai bada warantin kamoshi kuma ya bada umurnin a kawo shi gaban alkalin ko majistiren. A irin wannan hali, wanda ya tsaya mashi zai yi asarar kamuwar da aka rike mashi da nufin ta tabbatar da dawowarshi gaban kotu.

## MATAR MAI LAIFI A GABAN KOTU

Mata ko miji mai laifi ba zi yiwu a tilasta masu akan su bada shaida game da abokan auren su ba. Kuma ba za'a iya kama ta/shi da laifin taimakon mai laifin wurin tsere ma hukunci ba. Sabo da dokar 'yanci akan sirrin mutum tana aiki akan ganawar da suke yi a cikin auren su. Ba za'a kama mace da laifi akan laifin da mijinta ya tilasta mata ta aikata ba, ko laifin da yasa ta aikata a gaban idon shi sai dai idan laifin ya kunshi kisa ko raunatawa.

Ba za'a iya kama mace a tuhume ta a kotun da laifin satar dukiyar mijinta ba, sai dai idan sun rabu ne ko auren ya mutu.

## SA IDO DA RAKIYA WURIN SHARI'A.

Sa ido da rakiya wurin shari'a wasu abubuwa ne masu kama da juna, sai mutane daban ne suke yin kowane. Sa ido wurin shari'a shine halartar shari'a (wadda sau da dama ta laifi ce) ga lauyan daba tsaya ma wanda ake shari'ar dashi yake ba kai tsaye, sai dai yana lura da gudun ruwan al'amuran ne don tabbatar da ganin anyi adalci kuma an kare hakkin mai hakki. Ita kuwa rakiya wurin shari'a wanda ke yinta shine dan-agajin adalci, ko kuma duk mutumin da ke kusa, wanda zai iya bada karfin gwiwa da shawarwari ga wanda ake shari'ar da shi. A matsayin 'yan-agajin adalci, sau da dama zaku iya fuskantar bukatar rakiya ga wanda kuke hulda da shi zuwa kotu, ku jagorancesu game da yadda abubuwa ke tafiya, ku basu kwarin gwiwa sanan ku zama masu lura don tabbatar da anyi adalci. Musamman idan harkallar laifi ce to yana da kyau ku samu wakilin FIDA a wurin ya sa ido ga tafiyar shari'ar tun daga farko har karshe.

# BABI NA 9

## SAURAN AL'AMURA DA SUKA SHAFI MATA

## DANGANTAKAR MAIGIDAN HAYA DA DANHAYA

Kasancewar maigidan haya shike da mallakin gida bai bashi damar ya kwace gidan shi babu wani dalili ba ko kuma ya kara kudin haya babu dalili. Don ganin an kare dan haya daga shiga halin kaka-nika-yi, kuma a tabbatar da adalci a cikin dangantakar dake tsakanin dan-haya da maigidan haya, kuma a tabbatar da cewa dan haya bai rike kudin haya ko gidan hayar ba bisa ka'ida ba ko ya rika yin wasu abubuwa da suka saba ma doka a gidan, doka ta tsara sharuddan karbe gidan haya. Abun lura na farko shine a san cewa dangatakar tsakanin dan haya da maigidan haya yarjejeniya ce, don haka dole ne ta bi tsarin yarjejeniya.

Idan maigidan haya ya yanke shawara karbe gidanshi to doka ta wajabta mashi cewa ya ba dan haya masaniya da isasshen lokaci don kiyaye shi daga shiga halin kaka-nika-yi don ya samu damar samun wani gidan a natse.

Tsawon lokacin "Masaniyar Tashi" ya dangata da yanayin yarjejeniya hayar. Duk ta tanadi cewa:

- Mai gidan haya zai bada masaniyar tashi ga dan haya da ke biyan kudin haya a duk lokacin daya samu daman na tsawon sati daya.

- Maigidan haya zai bada masaniyar tashi ga dan hayar da ke biya wata-wata na tsawon wata daya.

- Maigidan haya zai bada masaniyar tashi ga dan hayar da ke biya bayan wata uku na tsawon wata uku.

- Maigidan haya zai bada masaniyar tashi ga mai biya shekara-shekara na tsawon wata shida.

Maigidan haya ba zai iya bada masaniyar tashi ga dan haya a cikin wa'adin kudin shi ba. Misali, Hamida tana haya a gidan Alhaji Yusuf tana biyan kudin haya wata-wata a ranar 15 ga kowane wata. A watan Mayu na shekarar 2010, sai ya yanke shawarar zai karbi dakin, sabo da danshi Aminu ya kamala karatunshi a jami'a, kuma Alhajin yana so ya bashi dakin shi na kanshi a gidan. To ba zai yiwu Alhaji Yusuf ya ba Hamida masani

‘yar tashi a ranar 10 ga watan mayu, kuma ya bukace ta da ta tashi a ranar 10 ga watan yuni. Dole ne masaniyar ta zo dai dai da karewar kudin hayar da ta riga ta biya.

**DOLE NE MASANIYAR TASHI TA KUNSHI WADANNAN ABUBUWAN:**

1. Sanarwa ga dan haya cewa ya tashi kuma ya mayar wa maigida gidanshi.

2. Adireshin gidan da ake so dan hayar ya tashi daga ciki.

3. Irin yarjejeniyar zaman haya da akayi da dan haya.

4. Ranar da ya biya kudin haya na karshe da kuma rana da zasu kare.

5. Ranar da wannan masaniyar tashi zata kare.

6. Sa hannun wanda ke bayar da wannan masaniyar, maigidan hayar ko wakilinshi ko lauyan shi.

Idan aka kai karshen kwanakin da masaniyar ke tasiri kuma dan hayar bai tashi ba daga gidan sai maigidan hayar ya bada rubutattar takarda da ke sanar da dan hayar kudurin maigidan na kwatar gidan shi cikin kwanaki bakwai bayyanannu, daga ranar da masaniyar tashi ta gama tasiri. (Ana kiran wannan takarda FOM E).

Misali, idan aka ba dan haya wannan takardar sanarwar kudurin kwace gida, a ranar litinin ta wannan satin, to wa’adin kwanaki bakwai zai kare ne a ranar litinin ta gaba da tsakar dare.

Bayan karewar wa’adin kwanaki bakwai, idan kan hayar ya ki tashi daga gidan to sai maigidan ya kawo mashi sammaci daga kotu irin wanda ake kira “FOM F”. Kotun da ta dace a yanko irin wannan sammace itace kotun wadda tafi kusa da gidan. dan hayar na da damar yin kara akan wannan kara bisa wani gyara da yayi ma gidan wanda ba’ai lissafin kudin gyaran cikin wa’adin zaman hayar ba, ko kuma duk wani abu da dan hayar ya kashe kudinshi akan gidan.

**YARJEJENIYA**

Yarjejeniya wata Magana ce da wasu mutum biyu ko fiye da haka suka yarje ma junasu game da wata mu’amilla wadda take da salon alkawari kuma za’a iya kama mutum da rashin cikawa a tsarin doka.

Yarjejeniya tana da salon alkawari sabo da doka ta shardanta ma bangarorin da sukayi yarjejeniya cewa dole su girmama yarjejeniya da duk kuma abubuwan da yarjejeniyar ta kunsa.

Ana iya kama mutum akan rashin cika maganar shi cikin yarjejeniyar saboda daya daga cikin bangarorin zai iya karar dayan bisa rashin cika sharuddan da ke cikin yarjejeniyar.

**YARJEJENIYA KASHI BIYU CE:**

**HUKUNTATTAR YARJEJENIYA-** Wannan itace irin yarjejeniyar da akan rubuta, a sa hannu a buga hatimi (idan dama ta samu) kuma a kiyaye ta. Doka ta bukaci cewa yarjejeniyar da ta shfi filaye da kamfanoni ta zamo an buga mata hatimi.

**YARJEJENIYA MAI SAUKI -** Yarjejeniya mai sauki itace wadda take zamowa a rubuce ko ta baki da baki.

**ABUBUWAN WAJIBI A CIKIN YARJEJENIYA**

Dole ne ingantattar yarjejeniya ta kunshi daya daga cikin wadannan abubuwan.

1. **FURUCI:-**Furuci shine wani cikakken alkawari da wani bangare yayi ga wani bangaren bisa kudirin cewa doka zata iya shiga ciki idan ya saba, kuma ana yinta a yayin da banagaren da ake yi ma wa ya amince. Dole ne furuci ya zama a fayyace, kuma a bayyane, kuma ba tare da rudani ba. Wanda yayi furuci ana kiranshi da suna mai furuci (offeror).

   A lura: Furuci kan Furuci – Idan wanda aka furta ma alkawari yaki karbar furucin, kuma yayi wani furucin da ya sha bamban da wanda aka yi mashi to irin wannan ake kira furuci kan furuci. Misali, idan "A" yayi furucin sayar da motar shi kirar Hummer Jeep akan kudi N350,000, sai "Z" ya bayyana ra'ayinshi akan cinikin to amma sai ya taya akan N250,000 ba wai N350,000 ba, to tayin nan da 'Z' yayi shine ake kira furuci kan furuci.

2. **YARJEWA:-** Bayan anyi furuci a fayyace to dole a samu yarjewa wadda zata yi ittifaki da sharuddan da ke cikin furucin, a rubuce ko ta baki wato (Parole). Wanda ya yarje ma furuci ana kiranshi hannun karba (**offeree**).

   Dole ne yarjewa ta zamo a fili, ba tare da tantama ba kuma ayi ta akan kari ga mai furucin kuma dole ne ta zama tana da cikakkar alaka da abin da akayi furuci a kanshi.. ba tare da abubuwa masu sanya salo ba, kuma ba tare da wani sharafi ba ko wani yanayi na musamman ba.

3. **BI-BAYA (CONSIDERATION):-** Bi-baya na da matukar muhimmanci a cikin yarjejeniya. Bi-baya tan nufin duk wata gajiya ko dawainiya ko wahala da ta hau kan mai furuci wurin cika sharuddan yarjejeniya (misali, wasu kudi da zai kashe ko wata dawainiya). Ba dole bane sai bi-baya ta zamo mai yawa. Misali 'A' ba zai yi korafin cewa kudin da 'Z' ya biya (N350,000) sunyi kadan bayan ya riga ya yarje da furrucin.

   A lura: Doka ta bukaci cewa a fitar da kimar bi-baya a tsarin doka. Duk yarjejeniyar da ke dauke da hatimi ba dole bane a yi mata bi-baya. Duk sauran yarjejejniyar da ba'a yi mata bi-baya ba to ba za'a iya yin kara akanta a kotu ba.

4. **KUDURIN HADA SHAR'ANTACCIYAR MU'AMILLA**

Dole ne duk bangarorin su dauki kudirin cewa shari'a ce zata yi aiki akan su cikin wannan mu'amilla. Misali idan Malam Audu ya yi ma matarshi Asabe alkawarin zai saya mata 'yan kunne da sarka idan ta haifi ka namiji, kuma yaki cika alkawarinshi, to Asabe ba zata iya yin karar shi a kotu ba domin babu abin da kotu zatayi akai sabo da babu kudurin shar'antarwa a cikin wannan furuci.

**ABINDA KE BATA INGANCI YARJEJENIYA:**

- **KUSKURE –** Idan mutum yayi furucin yarjejeniya a cikin kuskure.

- Kuskuren bayani ko kuskuren fahimta game da sigar abinda aka yi yarjejeniya a kanshi ko da abinda aka yi yarjejeniyar akanshi ko da kafin ko kuma a cikin lokacin da ake yarjejeniyar,wanda a dalilin haka daya bangaren ya shiga wannan yarjejeniya, ko dai sabo da fifikon matsayi da ke akwai akan wanda aka zambata.

- Mu'amillar da kan kunshi rashin dai-daito a cikin sharuddan yarjejeniya ta hada da tsakanin:

  - Iyaye da 'ya'ya
  - Mai riko da dan riko
  - Lauyan mutum da mutumin da yake karewa.
  - Likita da mara lafiya
  - Dalibi da malami
  - Dalibi (darami) da malami
  - Malamin addini da almajirinshi
  - Maigida da yaronshi.

- Yarjejeniya da ta haramta a doka itace duk yarjejeniyar da ke kunshe da abinda doka ta haramta. Irin wannan yarjejeniyar ana kiranta da sunan wadda ta saba ma shari'a kuma bata da wani tasiri ta kowace hanya. Misali irin wannan yarjejeniya itace amince ma juna don aikata laifi, amincewa wajen shigo da kayan hajar da doka ta haramta, amincewa don a zambaci gwamnati ko amincewa wurin habaka rashawa a cikin aikin gwamnati.

**ALURA**

Gaba daya dai ita yarjejeniya abuce wadda za'a iya yin shari'a akanta. Akwai wurare da dama inda ba za'a dauki yarjejeniya da siffar alkawari ba (sune haramtacciya ko rusassa haramtacciya tun asalinta). Yarjejeniyar da za'a iya haramtawa itace wadda keda yanayin zama haramatta (misali yarjejniya da karamin yaro, ko wanda ke cikin maye, ko mahaukaci, ko wanda bai iya karatu da rubutu ba).

Idan mutumin da bai iya karatu da rubutu ba ko makaho ya shiga wata yarjejeniya, to yana da kyau a samo shaidar shaida ga wannan mutum. Shaidar shaida wani rubutaccen ikirari ne wanda wani mutum daban da bangarorin zai yi kan cewa ya karanta ma makaho ko mara ilimin karatu da rubutun duk bayanan dake ciki yarjejeniyar, kuma sun nuna cikakkar gamsuwa da fahimtar yarjejiniyar.

**HUKUNCI**

Idan wani bangare ya saba ma yarjejeniya to daya bangaren (wato mai kara) na da wadannan hakkoki idan ya tabbatar da gaskiyar shi:

- A biya shi diyya bisa barnar da akayi mashi.
- Kotu zata bada umarni da a cika sharuddan kamar yadda akanyi yarjejeniya akai.
- Gindaya iyakoki da zasu hana wanda ya saba ya kara sabawa.
- Kotu za taba da umarni ga wanda ya saba da mayar, ko ya biya dai-dai da abinda ya saba ga wanda aka saba ma. Wannan shine ake kira "Kuantum Merit" a turance.

# BABI NA 10

**JERIN LITATTAFAN DA KE DA NASABA DA WANNAN LITTAFI**

**HAKKIN DAN-ADAM NA MATAKIN FARKO: BABI NA 4 TSARIN MULKIN NAJERYA NA 1999**

33,(1) Kowane mutum yana da ‘yancin rayuwa, kuma babu mutumin da za’a hana ma wannan hakki da gangan, sai dai wurin zartar da hukuncin kisa a kotu akan wani laifi da jerin manya-manya laifuka wanda aka tabbatar mutum ya aikata a Najeriya.

(2) Ba za’a dauka cewa an yiwa mutum kisan gilla ba wanda ya saba ma wannan sashe idan ya mutu a dalilin amfani da karfi daidai da wanda doka ta amince da shi kuma a irin yanayin da doka ta amince ayi kuma daidai kimar da doka ta amince ayi.

(a) Wurin kange mutum daga aikata haramtacciyar ta’addanci ko wurin kare dukiya;
.
(b) Wurin kokarin kare kama mai laifi bisa ka’ida ko wurin kange guduwar wannan mutumin da ke tsare bisa ka’ida; ko kuma

(c) Wurin kokarin murkushe tashin zaune-tsaye ko yunkurin juyin gwamnati ko tawaye ga doka.

34.(1) Kowane mutum na da hakkin a kiyaye mashi mutuncinshi da makamancin haka:-

(a) Babu mutumin da za’a azabtar ko ayi mashi wani abu na zubar da mutunci ko cin zarafu.

(b) Babu mutum da za’a bautar ko a tilasta shi bin umarnin wani ko bin ra’ayin wani ba bisa ka’ida ba.

(c) Babu mutumin da za’a tilasta mashi yin aikin karfi
.
(2) A dalilin karamin sashe (1) © na wannan sashe, aikin karfi na tilastawa bai hada da

(a) duk wani aikin karfi da aka sa mutum a dalilin hukunci ko umarnin kotu.

(b) duk wani aiki da aka sa wasu dakarun kasar nan ko jami'in hukumar 'yan sanda a wurin gudanar da aikin shi.

(c) ko kuma idan wani mutum yana da ja da ya danganci akidarshi game da abin da aka umarce shi a cikin aikin dakarun kasa duk wani aiki da aka sa shi a madadin abinda yake da ja akan shi

(d) duk wani aiki da aka sa mutum wanda ya zama wajibi a wurin wani aikin ceto kona yakar wata annoba da ke barazana ga rayuwar al'umma, ko

(e) duk wani aiki ko hidima da take daga cikin:

(i) aiyukan taimakon kai da kai don ci gaban al'umma

(ii) wata hidimar kasa ta wajibi a cikin aikin da karun kasa kamar yadda majalisar kasa ta bayyana; ko

(iii) wata hidimar kasa ta wajibi wadda take matsayin mahadi a tsarin karatu da horarwa ga dan kasa kamar yadda dokar majilisar kasa ta tanada.

35. (i) kowane mutum na da 'yancin walwala kuma babu mutumin da za'a hana ma irin wannan walwala face idan irin wadannan dalilai ne suka faru kuma bisa ka'idar da doka ta amince da ita:

(a) wurin yanke hukunci ko umarnin kotu kan wani laifi wanda aka tabbatar mutum ya aikata;

(b) A dalilin mutum ya kangare ma umarnin kotu wurin tabbatar da ya cika wani wajibabben hakki da dokar ta dora mashi;

(c) A dalilin kokarin gurfanar da shi gaban kotu saboda zargin ya aikata laifi, ko kuma a irin wannan hanyar, a wurin daya wajaba, wurin kange shi daga aikata laifi;

(d) Akan mutumin da bai kai shekara sha takwas ba, a dalilin karatun shi ko don tanadin inganta rayuwarshi;

(e) A kan mutumin da ke fama da cutar da ke yaduwa ta hanyar iska ko ta hanyar cudanya da mutane ko mutumin da keda tabin hankali, ko mutumin daya kamu da shan miyagun kwayoyi ko giya ko mutum dan zaman banza, a dalilin sama masu kula da maganin ko don kariya ga al'uma; ko

(f) don kange shigowar wani mutum cikin Najeriya ba bisa ka'ida ba ko don kokarin korar mutumin, ko mayar da mutumin kasar daya aikata laifi ko kuma don fitarwa daga Najeriya bisa wani dalili da doka ta yarda dashi ko a yayin da ake gudanar da shari'a akan mutum, wadda ta danganci irin haka.

Madamar mutumin da ake tuhumar da laifi kuma wanda aka tsare a bisa ka'ida don jiran shari'a ba za'a cigaba da tsare shi fiye da tsawon lokacin da za'a iya yanke mashi hukuncin zaman yari akan laifin da ake zargin shi da aikatawa ba.

(2) Duk mutumin da aka kama ko aka tsare yana da 'yancin yaki Magana, ko yaki amsa tambaya har sai ya gana da wani jami'in shari'a ko wani mutum da yake so ya gana da shi.

(3) Duk mutumin da aka kama ko aka tsare, to za’a sanar dashi a rubuce cikin awa 24 (kuma da yaren da yake fahimta) bisa dalilin kamashi ko tsare shi.

(4) Duk mutumin da aka kama ko aka tsare bisa ka’idar karamin sashe na (1) (©) na wannan sashe, to za’a gurfanar da shi gaban kotu cikin takaitaccen lokaci kuma idan ba’a yimashi haka ba cikin lokacin da ya kai

(a) wata biyu daga lokacin da aka kama shi ko aka tsare shi, game da mutumin da ke hannun hukuma ko wanda ba za’a iya bayar da belin shiba; ko

(b) wata uku daga ranar da aka kama shi ko aka tsare shi, game da mutumin da aka bada belin shi za’a sake shi (ba tare da la’akari da wata shari’ar da zai amsa a gaba ba) ko dai ba tare da wani sharadi ba, ko kuma bisa wasu sharuddan da suka wajaba don a tabbatar da ya sake dawowa gaban kotu don ci gaba da shari’a awani lokaci na gaba

(5) A cikin karamin sashe na (4) na wannan sashe, kalamin da akayi cewa “takaitaccen lokaci” na nufin

(a) Idan akwai kotu dake da hurumin irin hukuncin shi a kewayen inda aka kama ko aka tsare mutumin wadda bata wuce nisan kilomita arba’in ba, to tsawon kwana daya ne; kuma

(b) Idan ba haka ba, to tsawon kwana biyu, ko kuma tsawon lokacin da kotu zata iya duba a matsayin bai wuce ka’ida ba.

(6) Duk mutumin da aka kama ko aka tsare ba bisa ka’ida ba to yana da hakkin a biya shi diyya kuma a bashi hakuri a bainar jama’a daga hukumar da ta dace ko mutumin da ya dace; kuma a wannan karamin sashen, “hukuma ko mutumin da ya dace” na wanda doka ta bayyana.

(7) Babu wani abu daga cikin wannan sashe da za’a yi mashi daukar

(a) Dai dai da karamin sashe na (4) na wannan sashe, cewa yazo daidai da mutumin da aka kama aka tsare akan zargin ya aikata wani laifi daga jerin manya manya laifuka; kuma

(b) A matsayin rushe hukuncin dokar da akayi amfani da ita wurin tsarin tsare wani jami’i daga dakaran kasa ko jami’in hukumar ‘yan sanda har na tsawon lokacin da ya zarta wata uku, wurin yanke hukuncin da wani jami’i daga dakarun kasa ko na ‘yan sandan kasa ya kamashi dashi akan laifin da hukunci shi yayi daidai da haka.

36. (1) A wurin kokarin neman hakkin shi, kasancewar shi dan dasa, wanda ya hada da duk wata tambaya ko nema game da wata hukumar gwamnati, kowanne mutum na da hakkin a saurare shi da kunnen fahimta na tsawon lokacin da yai daidai da ka’ida a gaban kowace kotu ko kuma wata kotu ta musamman wadda doka ta kirkira kuma ta dora ta bisa turbar neman adalci.

(2) Ba tare da nuna son zuciya akan tanade tanaden wannan sashe ba, ba za’a rushe wata doka ba bisa dalilin taba wata hukumar gwamnati karfin ta warware wata matsala da ta

shafi ko kuma zata iya shafar ‘yancin wani mutum na zama dan kasa idan wannan doka ta:

(a) Bada dama ga mutanen da aka taba hakkinsu akan su yi bayani ga hukumar da ke zartar da wannan doka game da bukatun su da hakkokin su; kuma

(b) Ta kasance bata kunshi wani tanadi akan cewa hukuncin hukumar da ke zartawa shine hukunci na karshe wanda daga nan an yanke shawara.

(3) Shari’ar duk wata kotu ko kotu mai zaman kanta akan abubuwan da suka shafik karamin sashi na (1) na wannan sashe (har da sanarwar hukuncin kotu) zai kasance a bainar jama’a

(4) Duk lokacin da aka tuhumi wani jami’i da aikin laifi idan har ba’a janye wannan tuhumar ba, za’a bashi damar a saurareshi da kunnen basira a bainar jama’a a cikin lokacin da bai wuce ka’ida ba:

**madamar**

(a) Ita kotun zata fitar da duk mutanen da shari’ar bata shafe su ba, ko lauyoyin wadanda shari’ar ta shafa daga shari’ar don kiyaye tsaro, ko zaman lafiyar al’umma, ko bin doka, ko kiyaye tarbiyar al’umma, ko tabbar da kare lafiyar mutanen da basu wuce shekara sha takwas ba, ko kiyaye rayuwar mutanen da ke fuskantar shari’ar ko kuma a inda ya wajaba, sabo da wani yanayi wanda yasa yada labarin shari’ar bai yi dai-dai da bukatar adalci ba;

(b) Idan wata shari’a a wata kotu ko kotun musamman, wani minista na gwamnatin tarayya ko kwamishinan wata jiha ya bayyana cewa yin shari’ar a bainar jama’a ya saba wa bukatar zaman lafiyar jama’a, kotun ko kotun musamman din zata yi tanadin yadda za’a saurari shaidun wannan shari’a a asirce, kuma zata dauki matakin da ya wajaba don ta hana fasuwar sirrorin wannan shari’a.

(5) Kowanne mutum da aka tuhuma da aikata laifi za’a dauka cewa bashi da laifi har sai an tabbatar da laifin shi:

Madamar cewa babu wani abu a wannan sashe da zai rushe wata doka sabo da dokar ta dora ma wannan mutum wani nauyi wurin bincike kan wannan laifi.

(6) Kowane mutum da ake tuhuma da aikata laifi za’a ba shi damar:-

(a) Sanar dashi akan kari kuma da yaren da yake fahimta kuma da cikakken bayani, yanayin laifin da ake tuhumarshi da shi.

(b) A bashi isasshen lokaci da duk abubuwan da yake bukata don yakare kanshi.

(c) Ya kare kanshi da kanshi ko ta hanyar lauyan daya zaba.

(d) Ya binciki shaidun da mai gabatar da dara ya kafa akan shi ko da kanshi ko ta hanyar lauyan da ya zaba, kuma ya kawo nashi shaidun kuma ya binciki shaidarsu a

gaban kotun don su shaide shi a bisa irin sharadin da ya binciki shaidun da mai gabatar da kara ya gabatar; kuma

(e) Ya samu damar samun fassara daga tafinta idan baya fahimtar yaren da ake amfani dashi wurin gudanar da shari'ar ba kuma sai ya biya ba.

(7) Duk lokacin da aka gurfanar da wani mutum akan wani aikin laifi, to kotun ko kuma kotun musamman din zata adana bayanan wannan shari'a, kuma shi wanda ake tuhumar ko kuma duk wanda ya ba daman a iya samun kwafen shari'ar a madadinshi cikin tsawon kwanaki bakwai daga ranar da aka gama wannan harkalla.

(8) Babu mutumin da za'a kama da laifi bisa dalilin wata doka, ko wani sakin layi, wanda a lokacin faruwar wannnan abu babu dokar da ta kunshi irin wannan laifin, kuma babu wani horo da za'a dora akan wani laifi da wani ya aikata wanda ya zarta nauyin irin horon da ke aiki a lokacin da aka aikata laifin.

(9) Babu wani mutum da zai nuna cewa wata kotu ta taba gurfanar da shi, kotun kuma tana da hurumi akan wani aikin laifi kuma ta yanke mashi hukuncin horo ko ta tabbatar ba shi da laifi ta sake shi, kuma a sake gurfanar da shi akan wannan laifin sai dai idan wata babbar kotu ce ta bada umarnin haka.

(10) Babu mutumin da zai nuna cewa an yafe mashi bisa wani laifi da ya aikata kuma a sake gurfanar da shi akan wannan laifin.

(11) Babu mutumin da za'a gurfanar akan wani aikin laifi kuma a tilasta mashi akan ya bada shaida a cikin wannan shari'ar.

(12) Daidai da tanajin tsarin mulki, ba za'a yanke ma wani mutum hukuncin horo ba face idan wannan laifi ya kasance rubutacce a cikin rubutattun dokoki na kundin tsarin mulki, kuma a wannan karamin sashe, rubutattun dokoki na nufin dokokin majalisar wakilai, ko wani bangare daga cikin dokokin.

37. Sirrin kowanne dan kasa, da gidajensu, da huldodinsu, da firarsu ta wayar tarho, da ta na'urar tangaraho anan ya tabbata sirri ne kuma abin kiyayewa.

38.(1) Kowane mutum na da 'yancin bin ra'ayin shi, da irin imanin shi, da kuma addininshi, hadi da 'yancin sanya addini ko imani, da 'yancin nunawa da yada addini (ko da shi kadai ko kuma tare da sauran jama'a) yana iya yin haka ta hanyar ibada, ko koyarwa, ko ta bin tafarkin addini.

(2) Ba tare da son zuciya ba game da duk abin da ke cikin karamin sashe na (1) na wannan sashe ba, kowane mutum na da 'yancin ya mallaka ko ya kirkiro ko ya gudanar da duk wata cibiyar yada bayanai da ra'ayoyi;
Madamar cewa babu koma bayan Gwamnatin Tarayya, ko Gwamnatin Jiha ko wani mutum ko wata kungiyar mutane da Shugaban kasa ya bada izini bisa cika duk sharukkan da majalisar kasa ta shimfida, da zai mallaki, ko ya kirkiri, ko ya gudanar da gidan talabijin, ko tashar yada labaru ta sarari, koda da wane irin dalili ne.
(3) Babu wani abu daga wannan sashe da zai rushe wata doka wadda keda hujja a tsarin gwamnatin siyasa:

(a) Sabo da dalilin kange bayyana wasu labarai wadanda aka samu a asirce, tare da kiyaye hukunci da adalcin kotuna, ko tafiyar da harkar wayar tarho ko na'urar salula, ko yada labarai ta sarari ko ta talabijin ko majigi; ko kuma
(b) Gindaya iyakoki ga wasu mutane dake rike da ofishin gwamnatin tarayya ko ta jiha ko jami'ai daga dakarun kasa, ko jami'ai daga hukumar 'yan sanda ta kasa, ko wasu jami'an ma'aikatun tsaro wadanda doka ta kirkira.

40. Kowane mutum nada 'yancin shiga wani gangami a sake ba tare da kuntatawa ba, ya hada gwiwa da wasu mutane, kuma a takaice ma, yana iya kirkira, ko ya shiga wata jam'iyyar siyasa, ko kungiyar sana'a, ko kuma duk wata kungiya don kiyaye ra'ayinshi.

Madamar cewa tanade-tanaden wannan sashe ba zasu keta haddin hurumin da wannan tsarin mulki ya ba hukumar zabe ta kasa ba, dangane da jam'iyyun siyasar da hukumar zaben bata gamsu dasu ta basu izini ba.

41.(1) Kowane dan kasar Najeriya na da 'yanci yin zirga-zirga a sake a duk fadin Najeriya, kuma ya zauna a duk fadin kasar, kuma babu wani dan kasar Najeriya da za'a kora daga Najeriya ko a hana shi shigowa cikin kasar nan, ko fita daga cikinta.

(2) Babu wani abu a cikin karamin sashe na (1) na wannan sashe da zai rushe wata doka wadda keda hujja a tsarin mulkin siyasa:-

(a) Garkama takunkumi game da zama ko zirga-zirgar wani mutum da aikata, ko kuma ake kyautata zargin ya aikata wani aikin laifi don a kange shi daga barin najeriya; ko
(b) Don shirin dauke mutum daga najeriya zuwa wata kasa:-
(i) A gurfanar dashi gaban kotu a wajen najeriya saboda wani laifi daya aikata; ko
(ii) A saka shi gidan yari a wajen najeriya saboda hukuncin da aka kama shi da laifin aikatawa:
Madamar akwai yarjejeniya ciki da waje, tsakanin najeriya da wannan kasar game da wannan laifin.

42.(1) Babu wani dan kasar najeriya, dan wata al'uma dan wata kabila, dan wani jinsi, mabiyin wani addini,ko wani ra'ayin siyasa, don kasancewar shi haka, da za'a:-
(a) Sake shi kai tsaye, ko wurin zartar da wata doka dake aiki a najeriya, ko mataki daga wata hukuma, cikin wata alfarma ko fifiko wanda ba'a ba sauran 'yan kasar najeriya, yan sauran al'umma, da yaruka, da kabilu, da garuruwa, da jinsi, da addini, da ra'ayin siyasa ba.

(2) Babu wani kan kasar najeriya da za'a jaza ma wata nakasa ko rashi don kawai yanayin haihuwar shi.

(3) Babu wani abu daga wannan karamin sashe na (1) na wannan sashe da zai rushe wata doka bisa kujerar jagorancin wani ofishi a karkashin wata jiha ko taryya ko a matsayin jami'i cikin hukumar yan sandan kasa, ko kujerar wani ofishi na wata hukuma dokar najeriya ta kirkira.

43. Dai dai da tanadin wannan tsarin mulki, ko wane kan kasar najeriya, kowane dan kasa na da hakkin samu da mallakar kadara a duk fadin najeriya .

44. (1) Babu wata kadara ko kasa ko ba kasa ba da za'a kwace ma wani ta dole kuma babu wanda za'a hana ma hakki akan irin wannan kadara a ko ina a fadin najeriya sai dai

ta hanyar da doka ta amince kuma bisa dalilan da doka ta amince da su, cewa idan haka ta faru:-

(a) A biya diyya nan take kuma

(b) Mutumin dake neman irin wannan diyya na da yancin samun kiyasin diyyar da yawan diyyar a gaban kotu wata kotun musamman ko wata hukuma dake da hurumi a wannan bangare na Najeriya.

(2) babu wani abudaga karamin sashe (1) na wannan sashe da za’a yima daukar ya shafi wata doka ta game gari:-

(a) Don kagawa ko zartar da wani haraji, ko ushira, ko kudaden hukumar shige da fice,

(b) Don zartar da wani horo ko kwacewa a hukumance don horo a dalilin karya wata doka ko dai a tsarin dokar hakkoki, ko kuma ta laifuffuka;

(c) Abinda ya danganci bada hayar wani abu ko zaman haya ko jingina ko caji ko bil din cinikaiya, ko duk wani hakki ko wajabci daya shafi yarje jeniya.

(d) A binda ya shafi mallaki da gudanar wa game da wata kadara ta wani mutum wadda aka yanke hukunci ko kuma aka bada sanarwar cewa ta shiga bashi, kota wani mutum ce mara hankali ko wani mutum da ya mutu, kota wata hukuma ko kungiya ce wadda ke shirin rushewa;

(e) Abinda ya shafi yanke hukunci ko zartar da umarnin kotu;

(f) Don bada damar karbar mallakar wata kadara dake cikin wani yanayi mai hadari, ko wadda zata iya lahanta lafiyar dan-adam, ko tsirrai ko dabbobi.

(g) Abinda ya shafi kadarar kasar da ake gaba da ita;

(h) Abinda ya shafi iyakancewa cikin matakan da za’a iya dauka;

(i) Abinda ya shafi kadara mallakin wata hukuma wadda wata doka da ke aiki a Najeriya ta kirkira kai tsaye;

(j) Abinda ya shafi mallakar wata kadara na wucin-gadi don aune-aune da gudanar da bincike;

(k) Don bada damar yin aiki akan kasa don inganta nagartar kasa; ko

(l) Idan har an biya diyya kan kari game da barnar da aka yi ma gini, da itatuwan da ke samar da kudin shiga ko yabanya, wurin bada dama ga wata hukuma ko wani mutum ya shiga, ko ya yi safiyo ko yayi gini a wata kasa (fili) ko ya shimfida ko ya kafa falwaya ko wayoyi ko makwarari (fayif) ko wasu na’urorin isarwa ko wasu karafa akan wani filin kasa,don samarwa, ko gyara ko rarraba wutar lantarki, ko mai, ko iskar makamashi, ko ruwa ko bahaya, ko tarho, ko wasu aiyukan ci gaban al’uma.

(3) Duk da wadannan tanade-tanaden na wannan sashe, gaba-ayan kadarar da ke karkashin mallaki, ko karkashin kulawar wani, da duk ma’adanai, da ma’adanin mai, da sinadarin iskar gas, da ke cikin, ko karkashin ko akan wani filin kasa a Najeriya, ko rafukkan dake karkashin yankin Najeriya da kebantaccen yankin tattalin arziki mallakin

gwamnatin tarayyar Najeriya ne, kuma za'a gudanar da shi akan tsarin da majalisar kasa ta shirya.

45. (i) Babu wani abu daga cikin sassa na 37, 38, 39, 40 ko 41 na wannan tsarin mulki da zai rushe wata doka wadda keda hujja a tsarin mulkin siyasa.

(a) Don tabbatar da tsaro ko kiyaye lafiyar jama'a, ko tabbatar da bin doka da oda, ko tabbatar da tarbiyya, ko inganta da kiwon lafiya; ko

(b) A dalilin kiyaye hakki da 'yancin mutane

(2) Babu wata dokar majalisar kasa da za'a rushe a dalilin ta bada damar daukar matakan da suka saba ma tanade-tanaden sassa na 33 ko 35 a lokacin bukata ta gaugawa, to amma babu wani mataki irin wannan da za'a dauka wurin zartar da wata dokar majalisa akan wata bukata ta gaugawa face idan bukatar ta kai matukar da daukar wannan mataki a irin wannan yanayi bai ketara haddi ba a dai-dai wannan lokaci.

Madamar cewa babu wani abu na wannan sashe da zai bada izinin karya dokar da sashe na 33 na tsarin mulki, sai dai a dalilin mutuwa da ta faru lokacin yaki, ko ta bada izinin karya dokar sashe na 36(8) na wannan tsarin mulki.

(3) A wannan sashen "lokacin bukatar gaugawa" na nufin wani lokaci wanda a cikin shi akwai sanarwar yanayin bukatar gaugawa dake aiki a wannan lokacin wanda shugaban kasa ya bayyana, ta hanyar amfani da karfin dokar da yake dashi kamar yadda sashe na 305 na wannan tsarin mulki ya bashi.

46.(i) Duk mutum dake zargin cewa wani abu daga tanade-tanaden wannan babi, ya zamo ko zai iya zama an saba mashi a wata jiha game da shi kanshi, yana iya kai kara a wata Babbar Kotun jiha don neman hakki.

(2) Dai-dai da tanade-tanaden tsarin mulki, Babbar Kotu ita ke hurumi na ainifi ta saurari kuma tayi shari;a akan karar da aka yi mata don neman hakki da ke tsare a cikin wannan sashe, kuma zata iya bada umarni ko ta bada sammaci dai-dai da abinda taga ya dace wurin zartar da doka ko neman zartar da doka a wannan jiha, akan duk wani hakkin da mai karar yake dashi a tsarin wannan babi.

(3) Alkalin Alkalan Najeriya na iya yin wasu tsare-tsare game da aiki da kuma hanyar gudanarwar Babbar kotu game da abin da ya shafi wannan sashe.

(4) **MAJALISAR KASA:-**

(a) Na iya ba wata Babbar kotu karfin doka, kari akan abinda wannan sashe ya bata, idan majalisar kasa taga wajibcin yin hakan ko kyawun yanayi nayin haka don bada dama ga kotun ta yi amfani da hurumin da wannan sashe ya bata ta hanya mafi inganci; kuma

(b) Zata yi tanade-tanade

(i) Wurin bayar da taimakon kudi ga duk wani dan kasa kan asali idan aka taka hakkin shi kamar yadda yazo a wannan babi, ko don a bashi damar daukar lauya ya shigar da karar neman hakkin shi.

(ii) Don tabbatar da cewa zargin keta irin wannan hakki na bisa hujja mai karfi, kuma akwai tabbas game da bukatar taimakon kudi ko na ma'aikacin shari'a (lauya).

# BABI NA 11

**KAMU DA TSAREWA**

**SASSAN DA KE DA NASABA DAGA TSARIN MULKIN NAJERIYA NA SHEKARAR 1999**

35.(1) Kowane mutum na da 'yancin walwala, kuma babu mutumin da za'a hana ma irin wannan walwala sai dai a irin wadannan wurare kuma daidai da ka'idar da doka ta tanada:

(2) Duk mutumin da aka kama ko aka tsare yana da 'yanci yin shiru, ko yaki amsa duk wata tambaya har sai ya gana da wani lauya ko wani mutum day a zaba da kanshi.

(3) Duk mutumin da aka kama ko aka tsare to za'a sanar da shi a rubuce (kumada yaren da yake fahimta) cikin awa ashirin da hudu game da dalilan da suka sa aka kama shi ko aka tsare shi.

(4) Duk mutumin da aka kama ko aka tsare, daidai da tanadin karamin sashe na (1) © na wannan sashe, to za'a kawo shi gaban kotu cikin lokacin da bai wuce ka'ida ba, kuma idan ba'a gabatar da karar shi ba har tsawon lokacin day a kai.

(a) Wata biyu daga ranar da aka kama shi ko aka tsare shi, ga mutumin da yake a hannun hukuma, wanda ba'a bada belin shi ba; ko

(b) Wata uku daga ranar da aka kama shi ko aka tsare shi ga mutumin da aka bada belin shi, (ba tare da la'akari da wata shari'a da za'a iya kawowa game da shi ba) za'a sake shi, ko dai ba tare da wani shardi ba, ko kuma bisa wasu sharudda da suka wajaba bisa ka'ida don a tabbatar ya sake bayyana gaban kotu don sauraren shari'a.

(5) A karamin sashe na (4) na wannan sashe, cewa da aka yi "lokacin da bai wuce ka'ida ba" na nufin:

(a) Idan kamun ko tsarewar anyi tane a wani wuri wanda akwai kotu mai cikakken hurumi a kewayen nisan kilomita arba'in, to tsawon kwana daya ne; amma

(b) Idan ba haka bane, to tsawon kwana biyu ne, ko abinda ya wuce haka wanda yanayi zai sa kotu ta gamsu dashi bisa ka'ida.

(6) Duk mutumin da aka kama ko aka tsare ba bisa ka'ida ba, to yana da hakkin a biya shi diyya tare da ban hakuri a bainar jama'a daga hukumar da ta dace ko wani

mutum; kuma a wannan karamin sashe “hukumar da ta dace ko wani mutum” na nufin hukuma ko mutumin da doka ta bayyana.

36. (1) Wurin neman hakkin kasancewa dan kasa hadi da duk wata tambaya da duk wani neman kiyasi da aka yi ma mutum ko yayi ga wata gwamnati ko wata hukuma, mutum na da hakkin a saurareshi da kunnen basira na tsawon lokaci da bai wuce ka’ida ba, a gaban kotu ko kotun musamman wadda doka ta kirkira kuma doka ta tsara ta bisa turbar neman adalci.

(2) Ba tare da la’akari da tanade-tanaden wannan sashe ba wata doka ba zata rushe ba don kawai ta bada hurumi ga wata gwamnati ko hukuma dangane da warware matsaloli wurin zartar da wata doka wadda ta shafi, ko zata iya shafar hakkin wani mutum na kasancewar shi dan kasa idan wannan doka ta:-

(a) Yi tanadi game da damar mutumin da aka taba hakkinshi na ya bayyana kukanshi ga hukumar da ke zartarwa kafin wannan hukuma ta yanke shawarar da ta shafi hakkin wannan mutum. Kuma

(b) Bata kunshi wani tanadi game da daukar hukuncin wannan hukuma ya zama hukuncin karshe kuma abin yanke shawara akai ba.

(3) Shari’ar duk wata kotu , da kuma shari’ar duk wata kotun musamman game da abubuwan da aka fada a karamin sashe na (1) na wannan sashe (hadi da sanarwar yanke hukuncin kotu ko kotun musamman din) za’a yi sune a bainar jama’a.

(4) Duk lokacin da aka tuhumi wani mutum da aikata laifi, idan har ba’a janye tuhumar ba, za’a bashi damar saurare da kunnen basira a bainar jama’a cikin tsawon lokacin da bai wuce ka’ida ba, a kotu ko a wata kotu musamman.

Sai dai kuma:-

(a) Kotu ko kotun musamman din na iya tsame duk mutane daga shari’ar banda wadanda ake shari’a dasu ko lauyoyinsu sabo da dalilan tsaro, ko kiyaye lafiya al’umma, ko kiyaye bin doka da oda, ko kiyaye tarbiyar jama’a, ko kiyaye rayuwar wadanda basu jiba basu gani ba ko don wani dalili da ta duba bisa ka’ida, ya zama wajibi domin ganin wani yanayi na musamman wanda ya yada labarin shari’ar ya saba ma duk

(b) katar adalci;

(b) Idan a wurin wata shari’a a gaban wata kotu ko wata kotun musamman, wani ministan gwamnatin tarayya ko kwamishinan gwamnatin wata jiha ya gamsar da kotun ko kotun musamman din cewa bai yi dai-dai da bukatar jama’a ba idan aka bayyana sirrorin shari’ar kotun zata yi tattalin hanyar da za ta bi wurin sauraron shaidu a wannan sharia’ar a sirrance, kuma zata dauki duk matakin da ya wajaba don kare bayyanar sirrorin wannan shari’a.

(5) Duk mutumin da ake tuhuma da aikata laifi za’a dauka cewa bashi da laifi har sai in an tabbatar da laifinshi;

Sai dai kuma babu wani abu daga wannan sashe da zai rushe wata doka don kawai dokar ta dora ma mutum nauyin tabbatar da gaskiyar shi.

(6) Duk mutumin da ake tuhuma da aikata laifi yana da damar:-

(a) A sanar dashi a kan kari da yaren da yake fahimta kuma da cikakken bayani game da yanayin laifin da ake tuhumarshi a kai;

(b) A bashi isasshen lokaci da kayan aiki don ya shirya kariya.

(c) Ya kare kanshi da kanshi ko ta hanyar lauyan da ya zaba;

(d) Ya binciki shaidun da mai gabatar da kara ya kawo da kanshi ko ta hanyar lauyan shi, a gaban kotu kuma ya samu halartar shaidunshi da zasu bada shaidarshi, kuma ya bincike su a gaban kotu kamar yadda yayi ma shaidun da mai gabatar da kara ya gabatar;

(e) Ya samu taimakon tafinta ba sai ya biya ba, idan baya fahimtar yaren da ake shari'ar laifin dashi.

Babu wani mutum da za'a kama da laifi sabo da wata doka ko sakin layi wanda a lokacin da yayi abin, dokar bata kunshi irin wannan laifi ba, kuma babu wani horo da za'a dora ma wani laifi wanda ya zarta irin horon da ke aiki a lokacin da aka aikata laifi.

(9) Babu mutumin da zai bayyana cewar an taba tuhumarshi a kotu mai cikakken hurumi akan wani laifi ko da an kama shi da laifi ko ba'a kama shi da laifi ba, kuma a sake tuhumar shi akan laifin da ke da mahadi daya da wancan laifin sai dai bisa umarnin wata kotu babba.

(10) Babu mutumin da zai bayyana cewa an yafe mashi bisa wani aikin laifi kuma a sake tuhumararshi da wannan laifin.

(11) Babu mutumin da za'a tuhuma akan wani aikin laifi kuma a tilasta shi ya bayar da shaida a cikin wannan shari'a.

(12) Sai dai idan ba haka aka tanada ba a cikin tsarin mulki ba za'a hukunta mutum akan wani aikin laifi ba face an bayyana wannan laifin kuma an tanadi hukunci shi a rubutattar doka, kuma a wannan karamin sashe, "rubutattar doka" na nufin dokar majalisar wakilai, ko wani banagare karkashin tanade-tanaden doka.

**ALKAWARIN DUNIYA AKAN HAKKIN DAN KASA DA NA SIYASA (ICCPR)**

**SASHEN DOKA NA 9**

a. Kowa na da hakkin walwala da kariya ga kanshi. Babu wanda za'a kama ko a tsare ba dalili. Babu wanda za'a hana ma walwala sai dai bisa dalilin, kuma dai-dai da ka'idar da doka ta shimfida.

**b.** Duk wanda aka kama za'a sanar dashi, lokacin da aka kama shi din, dalilin kama shi kuma za'a sanar da shi duk wata tuhumar da ake mashi akan kari.

**c.** Duk wanda aka kama ko aka tsare bisa tuhumar aikata laifi za'a kai shi gaban alkali ko wani jami'i wanda ke da hurumin doka ga zartar da shari'a, kuma akan kari, sannan yana da hakki ayi mashi sharia'a cikin lokacin da bai wuce ka'ida ba, ko a sake shi. Ba zai zama doka magamiya ba cewa a tsare duk mutumin da yake jiran shari'a, to amma saki a gare shi ya danganta da tabbacin da aka samu cewa zai sake bayyana gaban kotu don ci gaban shari'a, a kowane mataki na shari'ar, ko kuma idan bukatar ta taso, don yanke hukunci.

**d.** Duk mutumin da aka hana walwala ta hanyar kamu ko tsarewa yana da hakkin ya kai shari'a gaban wata kotu don kotun ta tantance halaccin tsarewar da aka yi mashi ba tare da bata lokaci ba, ko ta ba da umarnin sakin shi idan tsarewar da aka yi mashi ta zama haramtatta.

**e.** Duk mutumin da ya fada cikin kamu ko tsarewa da take ba bisa ka'ida ba, to yana da hakki a gaban hukuma na a bashi diyya.

**SASHEN DOKA NA 10**

**1.** Duk mutanen da aka hana walwala to za'a rike su da mutunci kuma da girmamawa ga darajarsu ta dan-adam.

2.1 Face a wurare kebantattu, duk wanda ake tuhuma, za'a rarrabe shi daga wadanda aka tabbatar da laifinsu gaban kotu kuma aka hukunta su, kuma za'a rike shi da salo daban daga na wanda aka kama da laifi, dai-dai da kasancewar shi na wanda ake zargi.

2.2 Idan ana tuhumar yaron da bai balaga ba (bai shiga shekarun manya ba) to za'a rarraba shi daga manya, kuma za'a gaggauta gabatar da shi don shari'a.

2.3 Tsarin gidan yari zai bada yadda za'a riki 'yan fursuna, ya zama babban manufarta shine gyara dabi'u da ingata iya zama da mutane. Yaron da ya aikata laifi za'a rarrabe shi daga manya, kuma, za'a rike shi daidai da karancin shekarunshi da matsayinshi a idon shari'a.

**SASHEN DOKA NA 11**

Babu wanda za'a kai gidan yari don kawai ya kasa cika alkawarin da ya dauka a cikin wata yarjejeniya.

**SASHEN DOKA NA 14**

1. Dukkan mutane daidai suke da juna a gaban kotu ko kotun musamman. Wurin binciken tuhumar laifi akan mutum, kowa na da hakkin a saurare shi da kunnen basira, kuma a bainar jama'a a wata kotu mai hurumi, mai adalci wadda doka ta kirkira. Ana kebe sharia'ar ko wani bangaren na shari'ar daga 'yan jarida da sauran jama'a, sabo da dalilan kwanciyar hankali, da bin doka, da tsaro, a kasa irin ta mulkin siyasa, ko kuma don kare rayuwar wadanda ake shari'ar dasu idan bukatar haka ta taso, ko kuma idan kotu taga wajibcin haka a wasu wurare na musamman wurin fitar da bayanan shari'ar ya saba ma bukatar adalci; to amma duk wani hukunci da akayi akan wata harkalla laifi, ko game da kara akan doka to za'a yita a bainar jama'a sai dai idan ana kokarin kare bukatun yaro, ko kuma shar'ar ta shafi rigingimun ma'aurata ko rikon yara.

2. Duk mutumin da ake tuhuma da aikata laifi yana da hakkin a dauke shi matsayin mai gaskiya har sai an tabbatar da laifinshi ta tsarin doka.

3. A wurin kokarin binciken wata tuhumar aikata laifi akan mutum, kowane mutum na da damar a hore mashi akalla, wadannan abubuwa daidai da kowa:-

(a) A sanar da shi akan kari, da cikakken bayani da yaren da yake fahimta, game da yanayi da dalilin wannan tuhuma;

(b) A bashi isasshen lokaci da kayan aiki don shirya ma kariya;

(c) A yi mashi shari'a ba tare da jinkiri mara dalili ba;

(d) A yi mashi shari'a gabanshi, kuma ya kare kanshi ko dakanshi ko ta hanyar lauyan da ya zaba; kuma a sanar da shi idan bashi da lauya, cewa yana da wannan hakki; kuma a bashi lauyan da zai kare shi a duk inda bukatar adalci ta nemi hakan, kuma ba sai ya biya ba idan har ba shi da isassar hanyar da zai biya lauya;

(e) Ya bincika ko a bincikar mashi shaidun da aka gabatar a kanshi, kuma a nemi halartar shaidun shi tare da bincikar su don su ba da kariya a gare shi kamar yadda aka bada shaida akanshi;

(f) Ya samu taimakon tafinta kyauta idan baya fahimtar yaren da ake amfani da shi a kotun;

(g) Kada a tilasta mashi ya ba da shaida akanshi ko ya amsa laifin shi.

4. Idan ana shari'ar yaro to za'a bi hanyar da zata yi la'akari da karancin shekarun shi da kuma bukatar gyara halayyar shi.

5. Duk wanda aka tabbatar mashi da hannu kan aikata laifi to yana da hakkin wata babbar kotu ta sake duba hukuncin da aka yanke mashi bisa tsarin doka.

6. Idan aka yanke ma wani mutum hukunci akan ya aikata laifi kuma daga baya aka janye wannan hukunci ko aka yafe mashi sabo da wata sabuwar hujja, ko hujjar da aka gano daga baya ta nuna cewa anyi kuskure wurin shari'ar da akayi mashi, to mutumin da aka hora sabo da irin wannan hukunci za'a bashi diyya bisa tsarin doka, sai dai idan an tabbatar cewa rashin bayyanar wannan hujja akan kari daga gare shi ne gaba daya, ko kuma yana da hannu ciki;

7. Babu wanda za'a tuhuma ko a hukunta akan wani laifi wanda aka riga aka yi mashi hukuncin karshe akai ko aka sake shi sabo da bashi da laifi bisa tsarin doka da tafarkin hukunta masu laifi na kowace kasa.

**SASHEN DOKA NA 15**

1. Babu wanda za'a dauka a matsayin mai laifi akan aikata wani laifi wanda babu wata doka ko sakin layi da ya dauke shi a matsayin laifi, a tsarin dokar kasarshi ko duniya, a lokacin da ya aikata wannan laifin. Kuma ba za'a dora horon da ke aiki akan wani laifi, a lokacin da mutum ya aikata wannan laifi ba. Sabo da haka idan mutum ya aikata laifi, bayan wannan lokaci sai a ka yi tanadin wata doka don kara nauyin horo akan irin wannan laifi to mutumin zai amfana da hakan.

1. Babu wani abu daga wannan sashen doka da zai hana gurfanarwa da horon mutumin da ya aikata wani laifi, wanda a lokacin da ya aikata shi, laifi ne a tsarin doka ta game gari wadda wannan al'umma ta yarda da ita ko wadda duniya ta yarda da ita.

**YUNKURIN KAWAR DA DUK WANI BAMBANCI GA MATA (CEDAW)**

Matsayar Kasashe Mambobin Majalisa; tare da lura cewa kudin Majalisar Dinkin Duniya ya jaddada imani akan 'yancin dan Adam da kuma daraja da kimar mutum, da kuma dai daito tsakanin hakkin maza dana mata.

Tare da lura cewa furucin Duniya akan ‘yancin dan-adam ya jaddada kin karbar wariya kuma ya bayyana cewa duk ‘yan adam ana haihuwar su da ‘yanci kuma dai-dai da kowa a daraja da hakki, kuma na da damar samun kowane hakki da ‘yancin dake akwai ba tare da nuna banbanci ba ko wane irine, ko da kuwa banbancin jinsi ne
Tare da lura da cewa matsayar kasashe Mambobin Majalisa game da Alkwarin duk Duniya akan Hakkin dan adam na dauke da nauyin tabbatar da daidaito cikin hakkin maza dana mata don su fa’idantu da dukkan hakkoki, na bunkasa tattalin arziki, dana zaman takewa, dana al’adu, dana zama dan kasa da kuma hakkokin siyasa.

Tare da duba yunkurin duk duniya wanda aka kammala a karkashin tutar Majalisar dinkin Duniya, da hukumomi na musamman akan inganta daidaito tsakanin hakkin maza da na mata.

Tare da lura da mashalohi, da furuci, da shawarwarin da Majalisar Dinkin Duniya ta dauka da hukumomi na musamman don inganta daidaito tsakanin hakkin maza da na mata.

Tare da la’akari da duk da wadannan hobbasa da akayi, har yanzu ana ci gaba da nuna ma mata wariya, tare da tunawa da cewa, nuna banbanci ga mata ya saba ma manufar daidaito tsakanin hakkoki, ya kuma saba ma girmama darajar dan adam, kuma cikas ne ga yiwuwar mata su shiga a dama dasu cikin harkokin siyasa, zamantakewa, tattalin arziki da al’ada daidai da maza, kuma yana tauye habakar albarkatu acikin al’umma da kuma cikin iyalai, kuma yana sa irin gudummuwar da mata zasu iya badawa ga daukakar al’umma da kasarsu ta kara wahala.

Tare da nuna damuwa akan cewa, a yanayin tsanani, da talauci, mata su suka fi shan wahalar karancin abinci da kayan kiwon lafiya, da ilimi, da damar samun aikinyi da sauran bukatu.
Tare da gamsuwa akan cewa kirkirar sabon tsarin tattalin arziki na duniya akan ginshikin daidaito da adalci zai taimaka matuka wurin habaka daidaito tsakanin maza da mata.

Tare da karfafawa akan cewa kawar da ko-in-kula, da dukkan kabilanci, da bambancin launin fata, da mulkin mallaka da mulkin kama-karya, da zalunci, da mamayar kasashen ketare, da murkushewa, da katsalandan a cikin harkokin cikin gida na kasashe wajibine a cikin kokarin samun cikakkar fa’ida a hakkin maza da mata.

Tare da jaddada cewa karfafa zaman lafiya tsakanin kasashen duniya da kuma tsaro da kuma sasanta damarar fadace-fadace, da hadin kan kasashe ba tare da la'akari da tsarin tattalin arziki da tsarin zamantakewa ba, da jefar da makamai baki daya, musamman makamin are-dangi, a karkashin tsas-tsauran sa ido da kulawar duniya, da jaddada manufofin adalci, da daidaito, da fa'idantuwa da juna a tsakanin kasashe, da nuna sanin hakkin mutanen da suke karkashin kasar da ba tasu ba ko mulkin mallaka ko mamayar kasashen ketare da himmatuwa ga samun 'yancin kai da nuna girmamawa ga 'yancin mulkar-kai da dunkulewar kasa zai habaka ci gaban zamantakewa da bunkasar tattalin arziki, sannan adalilin haka za'a samu cikakken daidaito tsakanin maza da mata.

Tare da gamsuwa cewa cikakken ci gaban kasa, da habakar walwala a duniya da tafarkin zaman lafiya na bukatar shigowar mata daidai da maza a duk fannoni, tare da hasashen dinbin gudunmawar da mata ke bayarwa wurin jin dadi da walwalar iyali, da ci gaban al'umma, wadda har yanzu ba'a rika da cikakken muhimmanci ba, da irin muhimmancin kulawar uwa ga zamantekawar al'umma da rawar da iyaye ke takawa ga iyalai da tarbiyyar yara, tare da sanin cewar rawar da mata ke takawa wurin haihuwar 'ya'ya ba abinda za'a yi wariya a kanshi bane, sai dai tarbiyyar 'ya'ya na bukatar tarayya wurin daukar nauyi tsakanin maza da mata da kuma al'umma baki daya.

Tare da sanin cewa, akwai bukatar sauyi a cikin aiyukan mata da ayyukan maza a tsarin dabi'ar al'umma, kuma akwai bukatar daidaito tsakanin namiji da mace a cikin iyalai.

Tare da tamke damara don zartar da manufofin da aka shimfida a cikin furucin kawar da wariya ga mata, kuma don daukar matakan da suka wajaba don kawar da irin wannan wariya, koda wace iri ce kuma kota wane salo ta biyo, anyi yarjejeniya akan wannan.

**BANGARE NA 1**

**Sashen Doka na 1**

A manufar wannan yunkuri, kalamin "wariya ga mata" na nufin duk wani banbanci, ko fitarwa daga sahu, ko hani da akayi bisa la'akari da jinsi, wanda zai jaza, ko yake da manufar dakushewa, ko rushe izini, ko fa'idantuwa ko yunkurin aiki ga mata ba tare da la'akari da matsayinsu na aure ba,bisa dalilin daidaito tsakanin maza da mata da 'yancin dan adam da 'yanci na matakin farko a cikin fagen siyasa, ko na tattalin arziki, kona zamantakewa, kona al'ada ko na zama dan kasa koma kowane fage.

**Sashen Doka na 2**

Majalisa tayi Allah wadai da wariya ga mata ko wace iri ce, ta amince tabi duk hanyar da ta dace ba tare da jinkiri ba don kawo dokokin kawar da wariya ga mata don haka tayi alkawarin:

(a) Shigar da akidar daidaito tsakanin maza da mata a cikin kundin tsarin dokokin su da sauran dokokin majalisar wakilan kasashen su idan ba'a shigar dasu ba tun farko don tabbatar da samun cimma burin wannan doka a aikace ta hanyar dokoki da sauran hanyoyin da suka dace.

(b) Daukar matakan zartarwa da sauran matakai irin su kora daga aiki idan bukata ta taso, don haramta duk wata wariya ga mata.

(c) Kirkirar kariyar shari'a ga hakkokin mata daidai dana maza, don tabbatar da kariya mai tasiri ga mata daga duk wani aikin wariya ta hanyar kotuna musamman da sauran hukumomin gwamnati.

(d) Gujewa shiga cikin duk wani aiki na wariya ga mata don tabbatar da ganin cewe duk hukumomin gwamnati sun bi wannan wajibci.

(e) Daukar duk matakin daya dace don kawar da wariya ga mata daga duk wani mutum ko wata kungiya ko wata cibiyar huldodi.

(f) Daukar duk matakin daya dace kamar matakin zartarwa don gyarawa ko rushe dokoki ko hukunce-hukunce, ko al'adu ko wasu hanyoyin da ake aiki dasu wadanda suka kunshi wariya ga mata.

(g) Rushe duk wani hukuncin horo na kasa da ya kunshi wariya ga mata.

**Tsarin Doka na 3**

Kasashe Mambobin Majalisa zasu dauki duk matakin daya dace harda matakin zartarwa don tabbatar da ci gaban mata a fagen siyasa da zamantakewa da tattalin arziki da al'ada don ganin an basu damar shigowa ciki fa'idantuwa akan tafarkin daidaito da maza.

**Tsarin Doka na 4**

1. Daukar matakai na musamman ga kasashe yan majalisu da nufin tura wani daidaito na jeka-na-yika tsakanin maza da mata ba zai zama wariya ba kamar yadda aka bayyana a cikin wannan yunkuri, sai dai kuma bazai yiwu ya jaza ci gaban banbancin matsayi ba; wadannan matakai dole su tsaya a lokacin da aka samu cimma daidaito.

**Tsarin Doka na 5**

Kasashe mambobin Majalisa zasu dauki duk matakin daya dace:

(a) Don kawo sauyi cikin tsarin zamantakewa da na al’ada game da dabi’un maza dana mata, don ganin an cimma kawar da son zuciya da duk al’adu da sauran abubuwa wadanda aka kafa akan manufar kaskantarwa ko fifikon wani jinsi akan wani, da duk wani kallon raini a tsakanin maza da mata
(b) Dan tabbatar da cewa ilimin iyali ya kunshi cikakkar fahimtar tarbiyya da kaunar uwa ga ‘ya’yanta a matsayinsu na sinadarin kyakkyawar zamantakewa, da kuma bada daa ga mata da maza s dauki nauyi daidai da juna a wurin tarbiya da kula da ‘ya’yansu, ganin cewa bukatun ‘ya’ya sune abu na farko da za’a fara dubawa a ko ina.

**Tsarin Doka na 6**

Kasashe Mambobin Majalisa zasu dauki duk matakin daya dace, harda matakan zartarwa don dakushe fataucin mata da saka su hanyar karuwanci.

## BANGARE NA 2

**Tsarin Doka na 7**

Kasashe Mambobin Majalisa zasu dauki duk matakin daya dace don kawar da wariya ga mata a rayuwar siyasa da aikin gwamnati a cikin kasashen su, kuma zasu tabbatar ma mata hakkokinsu dai dai da maza a wajen:
(a) Jefa kuria wurin duk zabubbuka da wakilcin jama’a kuma basu damar tsayawa da cancanta a takarar kowane mukami na siyasa.
(b) Shiga a dama dasu wurin shirya manufofin gwamnati da zartar dasu, kuma su rike mukaman gwamnati kuma suyi duk irin aikin dake akwai na gwamnati kuma a kowanne mataki;
(c) Shiga a dama dasu cikin aiyukan kungiyoyin daba na gwamnati ba da kungiyoyin da suka shafi ayyukan jama’a da rayuwar siyasa a kasa.

**Tsarin Doka na 8**

Kasashe Mambobin Majalisa zasu dauki duk matakin daya dace don tabbatarma mata samun dama daidai da maza ba tare da wariya ba wurin wakiltar dasashensu a matakin duniya, kuma su shiga a dama dasu a cikin ayyukan kungiyoyin duniya.

**Tsarin Doka na 9**

1. Kasashe Mambobin Majalisa zasu bada hakki ga mata daidai da maza wurin samun izinin zama dan kasa, ko sauya kasar ko ci gaba da zama dan kasa. Zasu kuma tabbatar cewa auren bako (wanda ba dan kasa ba) ko barin kasa a dalilin aure ba zasu zama sun sauyawa mace kasa ba sai idan ta nemi sauyawa dakanta, haka kuma ba zasu sata zama bata da kasa ba, ba kuma zasu sa a cusa mata zama ‘yar kasar mijinta ba.
2. Kasashe Mambobin Majalisa zasu bada hakki ga mata daidai da maza game
3. dakasar ‘ya’yansu.

**BANGARE NA 3**

**Tsarin Doka na 10**

Kasashe Mambobin Majalisa zasu dauki duk matakin daya dace don kawar da wariya ga mata don a tabbatar masu daidaiton hakki tsakaninsu da maza a fannin karatu, kuma zasu tabbatar da daidaiton maza da mata wajen:

(a) Sharudda iri daya wurin zaben sana’a da samun kwarewa akan sana’a da kuma wurin karatu don samun takardun karatu daga kowace irin makaranta a yankunan karkara da birane; wannan daidaito zai tabbata tun daga kananan makarantu, da makarantun kwarewa a sana’a da manyan makarantun fasaha da kuma dukkan makarantun koyan sanin makamar aiki.

(b) Samun manhajar karatu iri daya, kuma jarabawa iri daya, kuma malamai masu takardun shaida iri daya, farfajiyar makaranta da kayan aiki masu inganci daidai da na maza.

(c) Kawar da duk wani kallon hadarin kaji acikin aiyukan maza da mata a dukkan matakai da dukkan salon tsarin karatu ta hanyar karfafa karatun da zai taimaka wurin cimma wannan buri, da kuma ta hanyar sake bitar littattafan karatu da tsare-tsaren karatu, da hanyoyin koyarwa.

(d) Samun dama daidai da juna wurin samun kudaden tallafin karatu da sauran kyaututtuka da ake ba ‘yan makaranta.

(e) Samun dama daidai da juna wurin samun ci gaba da karatu, har da karatun manya, musamman irin tsarin karatun da aka shirya da nufin gaggauta rage gibin dake tsakanin maza da mata ta fannin ilimi.

(f) Rage yawan barin makaranta ga dalibai mata, da kuma shirya wani shiri don yara mata da manyansu wadanda suka bar makaranta ba tare da sun kammala ba.

(g) Bada dama iri daya dan shiga da damawa cikin harkokin wasanni da motsa jiki.

(h) Samun bayanai na ilimi don su taimaka wurin tabbatar da lafiya da walwalar iyali hadi da bayanai da shawarwari wurin tsarin iyali.

**Tsarin Doka na II**

1. Kasashe Mambobin Majalisa zasu dauki duk matakin daya dace wurin kawar da wariya ga mata a fagen aiki don a tabbatar da hakki iri daya tsakanin maza da mata, musamman:

(a) Hakkin yin kwadago a matsayin shi na hakkin da ya wajaba a ba kowane dan Adam.

(b) Hakkin samun aikin yi daidai da juna, hadi da bin sharudda iri daya wurin zaben ma'aikata.

(c) Hakkin zabar sana'ar da rai ke so, da hakkin samun karin girma, da samun tabbacin dorewa cikin aiki da dukkan fa'idoji da tanadin da ma'aikaci kan samu, da hakkin samun horaswar sanin makamar aiki, harda horarwa ta dankoyo da horarwa ta kwararru da horarwa ta yau da kullum.

(d) Hakkin samun albashi daidai da juna har da sauran fa'idoji, da kuma samun riko iri daya a wurin aikin da yake iridaya da kuma daidaiton riko wurin duba ingancin aiki.

(e) Hakkin ingantattar zamantakewa, musamman a yayin aje aiki, ko rashin aiki, ko rashin lafiya, ko nakasa, ko tsufa kodai duk wani abu da kan sa mutum ya kasa aiki, da kuma hakkin biyan kudin hutu.

(f) Hakkin tsaron lafiya da kiyaye hadari wurin aiki, hadi da kiyaye aikin da nauyin shi ya rayata a wuyan mutum.

(g) Don kare faruwar wariya ga mata a dalilin aure ko daukar ciki, kuma a tabbatar masu hakkin yin kwadago, kasashe Mambobin Majalisa zasu dauki matakan da suka dace:

a. A haramta sa takunkumi, ko kora a dalilin hutun goyan ciki ko shayarwa da kuma wariya a wurin kora daga aiki a dalilin matsayin aure.

b. A shigo da tsarin hutun shayarwa tare da biyan kudin hutun, ko kuma wata fa'ida ta musamman ba tare da asarar aiki ba, ko fifikon girma ko alawus na zamantakewa.

c. A karfafa samar da hidimomi wajibabbu don tallafawa ga iyaye ta yadda zasu iya hada dawainiyar iyali da kwadago da damawa cikin aikin gwamnati, musamman ta hanyar kirkirowa da habaka wurare da abubuwan rainon yara.

d. A samar da kariya ta musamman ga mata a lokacin da suke dauke da ciki game da iri-iren ayyukan da zasu iya cutar dasu.

(3) Matakan zartarwa masu bada kariya game da dokokin da wannan bangare ya shata don su dace da hikimomin kimiya da fasahar zamani, kuma za'a rika bitarsu, ana gyarasu, kuma ana fadadasu yadda ya dace.

**Tsarin Doka na 12**

1. Kasashe Mambobin Majalisa zasu dauki matakin da ya dace wurin kawar da wariya ga mata a fannin kiwon lafiya, don tabbatar da samun aikace-aikacen kula da lafiya daidai da maza, harma da abubuwan da suka shafi tsarin iyali.
2. Ba tareda la'akari da tanade-tanaden sakin layi na 1 na wannan tsarin doka ba, kasashe Mambobin Majalisa zasu tabbatar ma mata dukkan taimakon daya dace game da daukar ciki da lokacin nakuda da lokacin shayarwa, kuma da basu taimako kyauta idan bukatar haka ta taso, tare da isasshen abinci mai gina jiki a lokacin goyon ciki da lokacin shayarwa.

**Tsarin Doka na 13**

Kasashe Mambobin Majalisa zasu dauki duk matakin da ya dace don kawar da wariya ga mata a sauran bangarorin tattalin arziki da na zamantakewa don tabbatar da samun hakkoki daidai da maza musamman:

(a) Samun hakkokin da ake ba masu iyali.

(b) Hakkin samun bashin banki da jingina da sauran fa'idoji na kudade da ake iya samu.

(c) Hakkin damawa cikin harkokin nishadi, da wasanni da sauran bangarorin rayuwar al'ada.

**Tsarin Doka na 14**

1. Kasashe Mambobin Majalisa zasu duba irin matsalolin da matan karkara ke fuskanta da kuma irin muhimmiyar rawar da matan karkara ke takawa wajen ceto tattalin arzikin iyalinsu, wanda ya hada da ayyukan da sukeyi wadanda bana kudi

bane, kuma zasu dauki duk matakan da suka dace don ganin anyi amfani da tanade-tanaden wannan yunuri ga matan karkara.

2. Kasashe Mambobin Majalisa zasu dauki duk matakin daya dace don kawar da wariya ga matan karkara don tabbatar da an basu dammar shiga a dama dasu kuma su ci gajiyar duk wani shirin bunkasa karkara dai dai da maza, musamman ma za’a tabbatar ma mata wadannan hakkin:

(a) Shiga su dama cikin harkokin fadadawa da gudanar da shirin bunkasa karkara a dukkan matakai.

(b) Samun wadatattun kayan kiwon lafiya, hadi da bayanai da shawarwari da taimakon tsarin iyali.

(c) Samun gajiyar kai tsaye daga shirye-shiryen inganta zamantakewa.

(d) Samun duk wata horarwa da koyarwa, na zamani dana al’ada hadi da abinda ya shafi koyan dabarun tafiyar da al’amuran yau da kullum da kuma kamar yadda aka bayyana a baya, duk wata gajiyar da al’ummar karkar ke iya samu dana fadadawa don samun Karin kwarewa wurin sana’a.

(e) Hada kungiyoyin hadin kai da taimakon juna don samun dammar habaka tattalin arziki ta hanyar kwadago ko sana’ar-kai.

(f) Damawa cikin dukkan hidimomin al’umma.

(g) Samun basussukan noma, da kayan kasuwanci, da fasahohin aiki na zamani da riko daidai da juna a fannin gona da gyara harkar noma da kuma shirin sake mazauni.

(h) Samun ingantaccen yanayin rayuwa musamman game da muhalli, da tsabtace muhalli da wutar lantarki da ruwa da sufuri da hanyoyin sadarwa.

**BANGARE NA 4**

**Tsarin Doka na 15**

1. Kasashe mambobin majalisa zasu ba mata matsayi daya da maza a gaban doka.
2. Kasashe mambobin majalisa zasu ba mata matsayin sharia daidai da maza a cikin tsarin zaman kasa, za’a kuma basu dama daidai da juna wurin amfani da wannan matsayi. Musamman ma za’a ba mata hakki daidai da maza wurin yanke shawara cikin yarje-jeniya, kuma su gudanar da dukiya, kuma za’a rikesu daidai da juna a duk matakan gudanarwa a kotuna da kotunan musamman.

3. Kasashe mambobin majalisa sun amince da duk wata yarje-jeniya da duk wasu takardun huldodi na jama'a wadanda suke da alaka da sharia, wadanda a ka yisu da nufin takura matsayin mata a idon sharia sun zama haramtattun.
4. Kasashe mambibin majalisa zasu ba mata da maza hakki daidai da juna wajen dokar data danganci tafiye tafiyen mutane da kuma 'yancin zabar mazauni da mahalli.

**Tsarin Doka na 16**

1. Kasashe mambobin majalisa zasu dauki duk matakin daya dace don kawar da wariya ga mata a cikin duk al'amuran aure da rayuwar iyali, musamman ma za'a tabbatar da daidaito tsakanin maza da mata a wajen:

(a) Hakki iri daya wurin zaben abokin zaman aure.

(b) Hakki iri daya wurin zaben abokin zaman aure da kuma dulla aure bisa yardarsu da ra'ayinsu.

(c) Hakki iri daya kuma nauyi iri daya cikin zaman aure da rushewar aure.

(d) Hakki iri daya kuma dawainiya iri daya a matsayin iyaye, ba tare da la'akari da matsayin aurensu ba, game da abinda ya shafi 'ya'yansu, ta kowane hali dai bukatun yaran sune mafi mahimmanci.

(e) Hakdi iri daya wurin yanke shawara game da yawan 'ya'yan da suke bukata da kuma tazarar dake tsakanin 'ya'yan, kuma su samu bayanai da ilmantuwa da hanyoyin da zasu basu dama aiwatar da wadannan hakkoki.

(f) Hakki iri daya kuma nauyi iri daya game da bada riko, da bada raino, da bada amana da kuma danko rikon 'ya'ya da duk abubuwa makamantan wannan a inda wadannan abubuwa ke tasiri a tsarin dokokin kasa, ta kowane hali dai bukatar 'ya''yan itace abin dubawa.

(g) Hakkin mutunci daidai da juna tsakanin miji da mata, wanda ya hada da hakkin zabar ladabin iyali da sana'a.

(h) Haki daidai da juna tsakanin ma'aurata wajen mallaka, da samu, da tattali, da gudanarwa, da cingajiya da juya kadara ko dai kyauta ko abisa mawa kika mai sauki.

2. Baiko da aurar da kananan yara zai zamo abu mara asali a dika, kuma za'a dauki duk matakin daya dace wurin kayyade karancin shekarun aure, kuma sanya rajistar aure a hukumance ya zama dole.

**BANGARE NA 5**

**Tsarin Doka na 17**

1. Domin duba yanayin ci gaban da ake samu wajen gudanar da wannan yunkuri za'a kafa kwamitin kawar da wariya ga mata (nan gaba za'a dinga kiranshi kwamiti) wanda zai kunshi kwararru masu kyawun hali da gogewa a fagen da yunkurin ya shafa, mutun sha takwas a farkon aikin yunkurin sannan kuma bayan kasashe sun rattafa hannu akai, wato kasashe talatin da biyar mambobin majalisa, za'a kara yawan 'yan kwamitin su kai ashiri da uku. Za'a zabo kwararrun 'yan kwamitin daga kasashe mambobin majalisa, kuma zasuyi aiki a matakan da suka dace dasu, za'a kuma yi kokarin zabo 'yan kwamitin daga kowane yanki na duniya kuma daga dukkan al'adu mabambanta na duniya kuma daga dukkan yankuna mabambanta a yanayin tsarin shari'a.
2. Za'ayi zaben 'yan kwamitin ta hanyar kuri'ar sirri wadda wasu ke bantattun mutane da aka wakilta daga kasashe mambobin majalisa zasu kada. Kowace dake da kujera a majalisa zata iya wakilta mutum daya daga cikin 'yan kasarta.
3. Za'ayi zaben farko bayan wannan yunkuri yayi wata shida da fara aiki. Kuma idan zaben ya rage saura wata uku, Babban Sakataren Majalisar Dindin Duniya zai aika wasika zuwa ga kasashe Mambobin Majalisa, yana bukatarsu dasu bada sunayen wakilan su a wurin zaben cikin wata biyu. Daga nan sai Babban Sakataren ya shirya sunayen wakilan daidai da harafin farko na sunayensu, tare da nuna kasar data wakilta kowanensu, sannan ya gabatar dashi gaban Majalisa.
4. Za'a yi zaben 'yan kwamitin ne a yayain wata ganawa da Babban Sakataren zai shirya a shalkwatar Majalisar dindin Duniya. A wurin ganawar, wadda hallatar kasha biyu bias ukun kasashe Mambobin Majalisa ya wadatar, duk wakilin daya samu kuri'u mafiya yawa kuma masu rinjaye daga masu kada kuri'a to yayi nasarar zama dan kwamitin.
5. Zababbun 'yan kwamitin zasuyi wa'adin shekara hudu. Sai dai kuma wa'adin mutun tara daga cikin 'yan kwamitin zai karene bayan shekara biyu dayin zaben farko. Za'a zabi sunayen wadannan mutum tara nan take bayan an kamala zaben, kuma shugaban kwamitin ne zai gudanar da zaben mutanen ta hanyar canka.
6. Za'a zabi sauran mutum biyar cikin 'yan kwamiti ta hanyar amfani da tanade-tanaden dake cikin sakin layi na 2, dana 3, dana 4 na wannan tsarin doka bayan kasa ta talatin da biyar ta rattafa hannu. Wa'adin mutum biyu daga cikin wadannan cikon'yan kwamitin zai kare bayan shekara biyu za'a zabi sunayen mutum biyun ta hanyar canka wadda shugaban kwamitin zai shirya.

7. A duk lokacin da aka samu wani gurbi a cikin kwamitin, to kasar da wa’adin wakilinta a cikin kwamiti ya kare itace zata nada wani kwararren daga ‘yan kasarta, tare da amincewar kwamiti.
8. ‘yan kwamiti zasu samu kudaden biyan su tare da amincewar jimillar majalisa, daga asusun majalisa, kuma bisa tsare-tsaren da majalisa ta amince dasu, tare da la’akari da muhimmiyar dawainiyar data rataya a wuyan kwamitin.
9. Babban Sakataren Majalisar dindin Duniya zai tanadi ma’aikata da kayan aiki don samun tasirin aiki da gudanar da dawainiyar kwamitin.

**Tsarin Doka na 10**

1. Kasashe Mambobin Majalisa sunyi alkawarin cewa zasu bada rahoto ga sakataren Majalisar Dindin Duniya game da tsarin zartarwa, da sharia, ta tafiyar da mulki da sauran matakan da suka dauka wajen tabbatar da tasirin wannan yunkuri da kuma ci gaban da aka sama akan:

(a) Shekaradaya da fara aikin wannan yunkuri a cikin kowace kasa.
(b) Bayan wannan kuma duk bayan a kalla shekara huku, da kuma duk lokacin da kwamiti ya bukaci haka.

2. Rahoton ya zama yana nuna abubuwan dake karfafawa da kuma wadanda ke da kushe cikar burin wannan yunuri.

**Tsarin Doka na 19**

1. Kwamiti zai shirya tsarin dokokin gudanar da aikin shi.
2. Kwamiti zai yi zaben mukaminshi na wa’adin shekara biyu.

**Tsarin Doka na 20**

1. ‘Yan kwamiti zasu rika ganawa na tsawon sati biyu ko kasa da haka a shekara don su duba rahotannin da aka tattara kamar yadda tsarin doka na 18 ya tanada a cikin wannan yunkuri.
2. Ganawar ‘yan kwimitin zata zama ana yinta a shalkwatar Majalisar Dindin Duniya, ko kuma a wani wurin da ya dace kamar yadda kwamitin ya amince (gyaran doka, matsayin rattafa hannu).

**Tsarin Doka na 21**

1. Kwamiti zai rika bada rahoto ga jimillar Majalisar Dinkin Duniya game da aikace-aikace kuma kwamiti zai bada shawara tare da hannunka mai sanda bisa ga

abinda rahotannin kasashe suka bayyana. Za'a hado shawarwarin kwamitin da hannunka mai sanda da sukayi a cikin rahoton da suka bada hadi da duk wani karin bayani da za suyi idan akwai shi.

2. Babban Sakataren Majalisar Dindin Duniya zai mika rahoton kwamitin ga hukumar tantance matsayin mata da sanin abinda ake ciki.

**Tsarin Doka na 22**

Hukumomi kwararru na musamman suna da hakkin samun wakilai a wurin dubawa da gudanar da tanade tanaden wannan yunkuri a wuraren da sukayi muwafaka da aiyukansu. Kwamiti zai gayyaci wadannan hukumomi don su mika rahotanni akan gudanarwar wannan yankuri a wuraren da suka shafi aiyukansu.

**BANGARE NA 6**

**Tsarin Doka na 23**

Babu wani abu a cikin wannan yankuri da zai canza duk wani tanadin da yafi wannan yunkuri tasiri wurin samun daidaito tsakanin maza da mata wanda ke cikin:

(a) Tsarin zartarwar wata kasa dake da wakilci a majalisa; ko

(b) Wani yunkurin daban na duniya, ko yarje-jeniyar kasa da kasa ko wata yarjewa dake aiki a cikin wata kasa mai wakilci a majalisa.

**Tsarin Doka na 24**

Kasashe mambobin Majalisa sun dauki alkawarin daukar duk matakin daya wajjaba a matakin kasa don cimma burin hakkokin da wannan yunkuri ya bayyana.

**Tsarin Doka na 25**

1. Za'a bude kofar sa hannu akan wannan yankuri ga kowace kasa dake da wakilci a Majalisa.
2. Babban Sakataren Majalisar Dinkin Duniya shine keda mukamin ma'aji a cikin wannan yunkuri.
3. Wannan yunkuri ya dogara ga rattafa hannun Kasashe Mambobin Majalisa. Za'a ajiye dukkan abubuwan da ake bukata wurin rattafa hannun a hannun Babban Sakataren Majalisar Dindin Duniya.

**Tsarin Doka na 26**

1. Dukkan kasashen dake da wakilci a majalisa zasu iya neman ayi bitar wannan yunkuri ta hanyar mika takardar bukata ga sakataren Majalisar Dinkin Duniya.
2. Gamayyar Majalisar Dinkin Duniya itace zata yanke shawarar matakan da za'a bi wurin yin wannan roko na bita.

**Tsarin Doka na 27**

1. Wannan yunkuri zai fara aiki a rana ta talatin bayan an kamala mika kayayyakin rattafa hannu na ashirin ga Sakataren Majalisar Dinkin Duniya.
2. Duk kasar da zata rattafa hannu kan wannan yunkuri bayan an riga an mika kayan rattafa hannu na ashirin ga sakatare, to yunkurin zai fara aiki gareta bayan kwana talatin da mika nata kayayyakin rattafa hannu.

**Tsarin Doka na 28**

1. Sakataren Majalisar Dinkin Duniya zai karbi, kuma ya raba ma kasashe masu kujera a majalisa, dukkan bayanan nuna ra'ayi da kasashe suka mika game da rattafa hannu kan yunkurin nan.
2. Duk wani nuna ra'ayi da akayi wanda yasha bamban da manufar wannan yunkuri to bazai samu karbuwa ba.
3. Za'a iya janye bayanin nuna ra'ayi da aka mika a kowane lokaci akaso yin hakan ta hanyar mika takardar sanarwa game da haka wadda za'a mika ga Sakataren Majalisar Dinkin Duniya, shi kuma zai sanar da kasashe masu wakilci game da haka. Wannan irin sanarwa zata fara aiki ne a ranar da aka karbe ta.

**Tsarin Doka na 29**

1. Duk wani sabani tsakanin kasashe biyu ko fiye masu wakilci a majalisa game da ma'aunin abubuwan dake cikin wannan yunkuri ko zartarwarshi wadda ba'a samu dammar warware shi ta hanyar tattaunawa ba, to za'a sasanta su a hukumance idan baya daga cikinsu yakai kukanshi akan haka. Idan har aka kai tsawon wata shida da kai koken ba tare da sun samu sasanci a tsakanin su ba, to kowane kaya

daga cikinsu zai iya mika al'amarin wannan sabani zuwa ga Kotun Duniya ta hanyar kai koke bisa tsarin wannan kotu.

2. Kowace kasa mai wakilci a Majalisa na iya bayyana bukatar cewa ita bata karkashin hukuncin da sakin layi na 1 na wannan tsarin doka a lokacin rattafa hannu kan wannan yunkuri. Sauran kasashe ma bazasu zamo a karkashin hukunci n wannan sakin layi ba dangane da duk kasar data nuna irin wannan ra'ayi.
3. Duk kasar data bayyana ra'ayinta bisa tsarin sakin layi na 2 na wannan tsarin doka to zata iya janye wannan ra'ayi a kowane lokaci ta hanyar rattafa hannu a wurin Sakataren Majalisar Dinkin Duniya.

**Tsarin Doka na 30**

Wannan yunkuri, wanda aka bayyana da larabci, da canisanci, da turanci da faransanci, da ranshanci, da yaren Spain wadanda duk kuma suke da ingantaccen asali daidai da juna, za'a ajiye su a wurin sakataren Majalisar dinkin Duniya.

**TARE DA SHAIDAWA AKAN HAKA**

mai cikakken ikon sa hannu yasa hannu akan wannan yunkuri.